# INA FATA
# ALLAH
# ZAI CECE NI

Daga Harold Camping



Ina Fata Allah Zai Cece Ni
(Hausa: I Hope God Will Save Me)
Daga Harold Camping

Waɗanda suka Buga;
Family Stations, Inc
Oakland, California 94621

Internet: www.familyradio.com
E-mail: international@familyradio.com

(A kula, dukan ayoyin da aka ambata a cikin
wannan Littafin daga Tsohon juyin Hausa
na Littafi Mai-Tsarki ne.)

11-17-2009

# ABINDA KE CIKI


**Gabatarwa** .... v

Ina Fata Allah Zai Cece Ni .... 1
Menene Allah Zai Yi Domin ya Ceci Wani? .... 3
Zaɓaɓɓe na Allah .... 4
An Bada zaɓaɓɓun Ga Kristi .... 6
Mai Ɗaukar Zunubi .... 6
Ɗumbin mutane waɗanda basu da Ceto tukunna
Waɗanda kuma Allah ba zai iya Hallakawa ba .... 8
Cikin Yanayin Mutuntaka, Dukan Mutane
matattu ne a Ruhaniya .... 9
Dole ne a Bamu Sabon Ruhu .... 10
Tabbacin Ceton Zaɓaɓɓu .... 12
Mu'ujjuzar Sabuwar haihuwa .... 13
Fassarar Da Littafi Mai-Tsarki ya ba Aiki na Ruhaniya .... 15
Kristi Ya yi Dukan Ayyukan da Ake Bukata
Domin Ceton mu .... 16
To Menene ya sa Allah ya bamu waɗannan Dokokin? .... 17
Dangantakar Allah Mai Ɗaurin kai da Mutum .... 18
Allah ya gwada Mutum .... 20
Babban Muhimancin Ranar Asabaci da Kwana na Bakwai .... 21
Albarkar da ke cikin Shirin Gwaji na Allah .... 22
Allah Yana Kara Tsananta Shirinsa na Gwaji .... 24
Zamu Iya Saurarон Littafi Mai-Tsarki ba tare da Mun ji ba? .... 26
Kwatanta Ayoyin Littafi Mai-Tsarki da Ayoyin
Littafi Mai-Tsarki .... 28
An Umurci dukan mutane da su Kira Bisa Sunan Ubangiji .... 30
Aikin Gaskantawa .... 32
An Umurci Dukan Mutane da su Gaskanta da Allah .... 35
Kristi Yayi Dukan Aikin- Ya yi Aminci-Domin Cetonmu .... 36
A Kowanne Lokaci, Allah ne ke Aikin Hatimcewa .... 37

Ba kowanne LOkaci ba ne yak an zama dole a yi gyara a fassara ba ........................................................................................ 38
Ko Ibrahim Ya Sami Ceto ne Sakamakon Gaskantawa da Allah? ........................................................... 40
Kristi na iya Ceton mu Idan muka Gaskanta da Shi ................. 42
Ruɗami a cikin Fahimtar kalmar nan ‘‘Gaskantawa’’ ............... 45
Shaiɗan ya zo kamar Mala’ikan Haske .................................... 46
Ko Akwai Yadda Za a Iya Kiyaye Tsarkin Ikklisiya? .................. 48
Babbar Sake Kama ................................................................. 50
Mutumin Da Ya Sami Ceto Yana Zaune a Gangar Jikin Da Bashi Da Ceto .................................................................. 51
Marmarin Mutum da Ya Sami Ceto ......................................... 53
Tsoro da Rawar Jiki ................................................................ 54
Cikakkar Kauna Tana Kawar da Tsoro .................................... 56
Ko Akwai Bege Domina? ........................................................ 59
Jerin Ayoyin Littafi Mai-Tsarki Da Aka Yi Amfani Da Su ..............

# GABATARWA

Mutane da dama suna cewa, ‘‘ Ina son in samu ceto.’’ Saboda haka a wannan ɗan littafin, zamu yi ƙoƙari mu fuskanci gaskiya zahiri, tambayar nan: Menene zan yi domin in sami ceto? Domin zamu gane cewa babu wanda zai iya yin wani abu da zai iya samun ceto, nan da nan zai sa masu karatu da dama su karaya waɗanda suka yanke hukumci cewa aikin banza ne, babu wanda zai sami ceto. Sai dai gaskiyar ita ce, lamarin mutanen da suke samun ceto a zamaninmu wani abu ne mai yiwuwa. Babu shakka kamar yadda muka yi nazarin Littafi Mai-Tsarki a hankali, mun gane cewa shaidun dake cikin Littafi Mai-Tsarki sun nuna cewa akwai babban girbi na mutanen da suke samun ceto a wannan lokaci a cikin tarihi.

Shaidar dake cikin Littafi Mai-Tsarki ita ce, a zamaninmu. mutane da dama suna samun ceto fiye da kowanne lokaci na tarihi. Amma ba suna samun ceto sakamakon bin wani tsarin ceto na wata Ikklisiya ba ko kuma kungiyar Ibenjelika wadanda ke neman shirin ceto a coci . Zamu koyi cewa yana da muhimmanci ainun cewa waɗanda suke koyarwa game da shirin Allah na ceto su yi da cikakken aminci da shirin ceton da Allah ya rubuta a cikin Littafi Mai-Tsarki.

# Ina Fata Allah Zai Cece Ni

Allah ya halicci duniyan nan wajen shekaru 13,000 da suka wuce. A wancan lokacin, faro daga kan iyayenmu Adamu da Hauwa'u, ya halicci mutum a cikin kamanninsa da kuma surarsa. Amma mutum yayi wa Allah tawaye, hukumcin wannan kuwa ya sa kowanne ɗan adam ya kasance a ƙarƙashin fushin Allah. Wannan tawayen yayi muni ƙwarai har a bisa dokar Allah, ba kasancewa har'abada tare da Allah mutum zai rasa kawai ba, amma za'a hallaka mutum gaba ɗayansa a rana ta ƙarshe ta kasancewar wannan duniyar. Sabili da haka mutane da yawa suka yi kuka, "Ina bukatar a cece ni daga wannan hukumcin na lalacewa ta har abada."

Kowane mutum yasan akwai Allah, ya kuma sani cewa zai bada lissafin zunubansa ga wannan Allahn. Wannan ya faru ne domin an halicci mutum a cikin kamanni da kuma surar Allah. Kuma ko da yake mutum yayi nisa da Allah sabili da tawayen da yayi wa Allah, Sanin Allah da kuma sanin cewa zai bada lissafi ga Allah yana nan a cikin rayuwar sa. Mun karanta Romawa 2:13-15, a cikin waɗannan ayoyin, kalmar nan "Al'ummai" tana nuni ne ga dukan mutanen duniya waɗanda basu da ilimin Littafi Mai-Tsarki.

**Gama ba masu jin doka ne masu kuɓuta ga Allah ba, amma masu aika doka za su kuɓuta: gama Al'ummai, waɗanda ba su da shari'a, kadan bisa ga tabi'a su ke aika abin da ke na shari'a, waɗannan domin ba su da shari'a sun zama sharia ga kansu; da shi ke suna bayan aikin shari'a a rubuce cikin zukatansu, lamirinsu kuma yasa suna kai ƙara ko kwa suna kawo hujja.;**

Sabili da haka, dukan mutane sun sani cikin lamirinsu cewa zunubi ne, wato tsallake shari'ar Allah ne mutum yayi kisan kai, yayi sata, yayi zina, da dai sauransu. Ya kuma sani a cikin lamirinsa cewa Allah zai hukumta zunubai. Wannan shi ya sa

dukan ’yan adam suke neman hanyar yin sulhu da Allah. Wato, yana neman hanyar da zata kuɓutar da shi daga mugun horon nan da ke zuwa sakamakon zunubansa.

Waɗansu suna ƙoƙari su warware wannan matsalar ta wurin rarrashin kansu cewa babu Allah wanda zasu tsaya a gabansa. Waɗannan suna iyakacin ƙoƙarin su su ce babu Allah ko kuma su ɗauki wani matsayi da zai wofintar da duk wata magana game da Allah.

Waɗansu kuma sun ƙerawa kansu allolin da suke bautawa. Sun yi Allah na itace ko dutse, kamar su Budis, ko kamar masu bautawa taurari, sukan dubi sararin sama da taurari a matsayin wani allah, ko kuma wasu mutane da yawa da suka sami wani addini wanda suke jin daɗin aikatawa. Wannan addinin bashi da wata dangantaka da Littafi Mai-Tsarki, ko kuma zai iya yin amfani da waɗansu ayoyin Littafi Mai-Tsarki domin ya sami goyon baya daga garesu. Ta haka, sai su sami addinin da a ganinsu, zai iya sulhuntasu da Allah.

Gaskiyar ita ce, a yau, kusan kashi ɗaya bisa uku na dukan mutanen da ke a duniya suna kiran kansu “Masu bi.” Wannan na nufin suna riƙe da wani addini wanda yake amfani da wani sashe na Littafi Mai-Tsarki domin su ƙarfafa cewa wannan ita ce Bisharar da zata kai mutane wurin Allah. Kowane addini, koda dangantakarsa da Littafi Mai-Tsarki ’yar ƙanƙanuwa ce ko kuma yana riƙe da gaskiyar Littafi Mai-Tsarki ne, yana iƙirarin cewa sune ke bisa hanyar samun sulhu da Allah mafi daidai. Haka yake ga sanannun ɗariku kamar su Roman Katolika, Baptist, Reform, Presbitarian, Masu kiyaye Ranar Asabaci, Jahoba witness, Mormon da dai sauransu. Abin baƙin cikin shine ba ko ɗaya daga cikin waɗannan ɗarikun wanda yake da cikakken sanin yadda ake samun sulhu da Allah ko kuma abin da mutum yake bukata domin ya sami sulhu da Allah, wato, ya sami ceto daga fushin Allah, wanda kuma shine hukumcin zunuban da ya aikata.

*Abin baƙin cikin shine waɗanda suka kafa begen samun ceton su a cikin ɗaya daga cikin addinan nan har yanzu suna cikin babbar matsala da Allah domin addininsu ba zai cece su ba.*

Abin baƙin cikin shine waɗanda suka kafa begen samun ceton su a ɗaya daga cikin addinan nan har yanzu suna cikin babbar matsala da Allah domin addininsu ba zai cece su ba, kuma basu sauraron kaɗaitacciya tushen hanyar gaskiya, wato Littafi Mai-Tsarki.

A cikin wannan ɗan littafin, gwargwadon iyawata, zan yi ƙoƙari in fito da abin da Littafi Mai-Tsarki yake koyaswa game da shirin Allah inda mutane da yawa suke samun sulhu da Allah suke kuma samun tserewar wannan mummunan hukumcin da zai sabko bisa dukan 'yan adam a ƙarshen duniya.

Mu tuna cewa a cikin harshen rubutunsa na farko, Allah ne ya rubuta shi, sai dai yayi amfani da mutane marubuta kamar yadda 2 Bitrus 1:21 ta faɗa mana:

**Gama ba a taɓa kawo kowane annabci bisa ga nufin mutum ba: amma mutane suka yi magana daga wurin Allah, Ruhu Mai-Tsarki ne yana motsa su.**

Kalmomin da suka zana, kalmomi ne da Allah da kansa ya faɗa (Irmiya 36:1-4). Sabili da haka, muna samun ƙashin gaskiya ta wurin karatu da binciken Littafi Mai-Tsarki. Sabili da haka, dole ne kowane matsayi da za'a ɗauka game da shirin Allah na ceto yayi daidai da abin da Littafi Mai-Tsarki ke koyaswa. Sabili da haka, ya kamata mu kasance a shirye mu binciki kowane matsayi da mutum ya ɗauka bisa ga koyaswar Littafi Mai-Tsarki.

### *Menene Allah Zai Yi Domin Ya Ceci Wani?*

Zamu ci gaba da binciken mu ta wurin tabbatas da abin da Littafi Mai-Tsarki ya furta game da mafita daga mummunan halin da mutum ya sami kansa a ciki. Zamu gane cewa yanayin da mutum ya sami kansa a ciki yayi muni ƙwarai har ya zama Allah ne kaɗai zai iya tanada hanyar tsira.

Mu tuna cewa Littafi Mai-Tsarki gaba ɗayansa, littafi ne na shari'a wanda Allah da kansa ya rubuta, wanda kuma dole ne kowane ɗan adam yake ƙarƙashi, Allah ma da kansa yana biyayya da shi (Zabura 138:2). Sabili da haka dole ne a nemi maganin matsalar da mutum ya shiga a cikin littafin shari'ar Allah, wato Littafi Mai-Tsarki.

Akwai muhimman matakai guda uku da Allah da kansa ya ɗauka waɗanda suka zama dole kafin wani ya iya samun ceto a cikin rayuwarsa. Ana kuma buƙatar kowane mutum wanda ya sami ceto ya ɗauki waɗannan matakan. Ba wanda aka ware.

### *Zaɓɓaɓɓe na Allah*

Abu na farko da Allah yayi a madadin dukan mutanen da za'a ceta shine, tun kafin kafawar duniya, Allah ya zaɓi dukan mutanen da zai ceta. Mun karanta a Afisawa 1:3-5 cewa:

**Albarka ga Allah Uba na Ubangijinmu Yesu Kristi, wanda ya albarkace mu da kowace albarka mai ruhaniya cikin sammai cikin Kristi. Kamar yadda ya zaɓe mu a cikinsa gaban kafawar duniya, domin mu kasance masu tsarki marasa aibi a gabansa cikin ƙauna: bayanda ya rigaya ya ƙadara mu mu zama 'ya'yansa ta wurin Yesu Kristi, bisa ga yardan nufinsa.**

Yayinda Allah yake shirin halittar wannan duniya da biliyoyin mutanen da ke cikinta, ya duba jerin zamani ya hangi ɗinbin jama'a cike da baƙin ciki waɗanda suke rayuwa cikin tawaye ga Allah. Ko da yake Allah ya halicci mutum mara aibi, a cikin kamanni da surar Allah, Littafi Mai-Tsarki ya bayyana a sarari cewa Allah ya sani cewa mutum zai yi wa Allah tawaye, wannan tawayen kuwa zai haifar da mutuwa ta ruhaniya ga dukan mutane waɗanda zunubi ya mamaye. Allah kuma ya sani cewa mutum zai yi iyakacin ƙoƙarinsa ya yi sulhu da Allah ta wurin neman Allah a cikin shirye shirye waɗanda suka fito daga cikin zuciyar mutum, wadda take cike da zunubi, amma ba wanda zai nemi Allah bisa ga sharuɗan da Allah ya gindaya.

> *Allah kuma ya sani cewa mutum zai yi iyakacin ƙoƙarinsa ya yi sulhu da Allah ta wurin neman Allah a cikin shirye shirye waɗanda suka fito daga cikin zuciyar mutum.*

A cikin Romawa 3:10-12, Allah ya bayyana irin abin tausayin da yanayin mutum ya zama. A wurin mun karanta cewa:

**Kamar yadda an rubuta, Babu mai-adalci, ko ɗaya; babu mai fahimta, babu mai neman Allah; Dukansu sun ratse, sun zama marasa amfani baki ɗaya; babu wani mai aika nagarta, babu ko guda ɗaya.**

Amma duk da wannan lalacewar da tawayen mutum ga Allah ya jawo, Allah yayi shawara mai ban mamaki cewa zai zauna da mutane masu tawaye da yawa har abada. Amma ta yaya zai iya kasancewa da mutanen nan har abada? Hukumcin zunubansu yana da nauyi ƙwarai, Ta yaya Allah zai iya kasancewa har abada da mutanen da dole ne a hallaka su sabili da zunubansa. Hukumcin zunubi mummuna ne domin zunubin mutum mummuna ne. Daga nan ne shahararren shirin ceton mutane na Allah ya taso.

Sabili da haka ba kawai Allah ya zaɓi waɗanda zai baratas domin kansa tun kafin kafawar duniya (Afisawa 1:4) kaɗai ba, amma ya biya bashin zunubansu. Ko kaɗan zaɓin shi bai kafu akan wani aiki ko wani marmari na mutum ba. A cikin Romawa 9:15 Allah ya ce:

**... Ni yi jinƙai kan wanda na jiƙansa, ni yi tausayin wanda na yi tausayinsa kuma.**

Ta wurin sanar mana da wannan aiki na farko da Allah yayi, Allah ya kawo bege ga dukan mutumin da bashi da ceto. Allah ya tsaya akan cewa shi ba mai tara ba ne (Romawa 2:11; Afisawa 6:9; Kolossiyawa 3:25). Ba wata ƙasa ko jinsin mutane da za'a ce zasu fi kowa yawa a cikin zaɓaɓɓu na Allah. ba wata ƙungiyar masu zunubi da za'a ce tafi wata nisa da kasancewa cikin zaɓaɓɓu na Allah.

A cikin Yohanna sura 8, Littafi Mai-Tsarki ya bada labarin ceton wata mata mazinaciya, a cikin Luka 23:9-43 kuma ya bada labarin ceton wani mafashi da aka giciye tare da Yesu. Sabili da haka, kome girman zunubanmu, idan muna da marmarin ceto bisa ga sharuɗan Allah, muna da damar kasancewa a cikin zaɓaɓɓu na Allah. Ganin cewa a yau ɗinbin mutane suna samun ceto, yana yiwuwa nima zan iya kasancewa ɗaya daga cikinsu. Wannan babban abin ƙarfafawa ne.

*An Ɓada Zaɓaɓɓun Ga Kristi*

An ba Ubangiji Yesu Kristi waɗanda Allah ya zaɓa ya ceta kamar yadda muka karanta a Yohanna 6:37:

**Dukan abin da Uba ya bani za ya zo gareni; wanda ya zo gareni kwa, ba ni fitar da shi ba ko kaɗan**

Amma kafin Yesu ya iza samun waɗannan zaɓaɓɓun a matsayin nasa, dole ne sai an yi wani abu game da zunubansu. Cikakkar shari'ar Allah wadda Allah ne da kansa ya rubuta ta zartas cewa domin an halicci mutum a kamannin Allah, dole ne kowane ɗaya ya biya bashin zunubinsa kamar yadda shari'ar Allah ta nema a yi. Sabili da haka, koda shike Allah ya zaɓe su ya kuma ba Kristi domin su zama nasa har abada, Kristi ba zai iya samun su ba sai an biya bashin zunubansu. Shari'ar Allah ta furta cewa hakin zunubi mutuwa ne, sabili da haka, waɗanda aka zaɓan nan aka ba Kristi ba zasu iya zuwa ga Kristi a matsayin nasa ba domin ba zasu iya biyan bashin zunubansu ba. Wannan ya kawo mu ga wani muhimmin abin da Allah yayi a madadin dukan waɗanda suka sami ceto.

*Mai Ɗaukar Zunubi*

Sa'adda Allah yake duban duniya wadda yake shirin kafawa a farkon zamani, ya lura cewa babu wanda zai yi amfani da shi domin ya ɗauki zafin fushin Allah a madadin zaɓaɓɓu, waɗanda Allah ya zaba ya kuma ba Kristi a matsayin abin gadonsa na har abada. Ishaya 63:5 da Ezekiel 22:30 sun koyas mana da haka. Sai dai kuma, dokar Allah wadda bata da aibi ta zartas cewa dole ne a biya hakin zunubi da mutuwa kafin kowane mutum ya iya shiga sama ta Allah mai-tsarki. Dole ne a cika kowanne sashi na dokar Allah wadda take cikakka.

*Sabili da haka, a cikin jinƙai da ƙauna wadda babu irinta, Kristi da kansa ya zamo mai ɗaukar zunubi a madadin waɗanda aka bayar a gareshi.*

Sabili da haka, a cikin jinƙai da ƙaunar wadda babu irinta, Kristi da kansa ya zamo mai ɗaukar zunubi a madadin waɗanda aka bayar a gareshi. Mukan karanta wannan a cikin Ishaya 53:6.

**Dukanmu kamar tumaki muka ɓata, kowanne ya karkace garin bin nasa tafarkin, sai Ubangiji ya sa hukumci ya sauko a kansa, hukuncin da ya wajaba a kanmu.**

Kalmar nan "duka" tana magana ne akan dukan zaɓaɓɓu, wato, dukan waɗanda Allah ya zaɓa su zama cetattu tun kafin kafawar duniya. A gaskiya ma, ya rigaya ya biya bashin zunubansu tun kafin ya kafa duniya. A cikin wata koyaswa (misalai na tarihi) Kristi ya nunawa duniya yadda dole ne ya sha wahala domin biyan bashin zunuban zaɓaɓɓu. Za'a iya ganin wannan cikin irin wahalar da ya sha a lokacin da aka giciye shi. A misali, an rataye shi a bisa giciye cikin ƙasƙanci domin a nuna cewa dole ne ya zamo la'ana domin ya iya biyan bashin zunubi. "La'ananne ne dukan wanda aka rataye a itace." Lokacin da aka sa jikinsa a cikin kabari ya kuma tashi a ranar Lahadi da safe, wannan ma wani nuni ne na cewa ya biya bashin zunubanmu ta mutuwa tun kafin kafawar duniya, ya kuma tashi domin ya nuna cewa an gama aikin biyan bashin zunubanmu. (Dubi Ɗaukaka Ga Allah).

Lokacin da Kristi yake kawo ceto ga zaɓaɓɓu, an ɗora dukan zunuban dukan mutanen da ya yi niyyar ya ceta a bisansa. Ɗauke kuma da wannan nauyin kayan zunubin, ya tsaya a gaban Allah Mahukumci domin a yi masa shari'a, an kuma same shi da laifi. Domin a cika abin da shari'ar ta nema, ya zama masa dole ya ɗauki dukan horon da shari'ar ta zaiyana a madadin kowane ɗaya daga cikin waɗanda ya so ya ceta. Wannan horon kuwa shine mutuwa: "... wanda yayi zunubi, shi zashi mutu" (Ezekiel 18:4b). Haka kuma mun karanta cewa "Ba zaka bar raina ya ga ruɓa ba." Wannan ya nuna cewa Kristi ya mutu ya kuma tashi tun kafin ya halicci duniya. Yadda aka gudanar da wannan duka yana ɓoye cikin al'amuran asiri na Allah.

Akwai mutane da yawa a cikin wannan duniya waɗanda aka zaɓa domin ceto aka kuma miƙawa Kristi su a matsayin nasa har abada. Domin Yesu Kristi ya zama Mai Cetonsu ta wurin biyan bashin zunubansu, sun zama keɓaɓɓu har abada tun kafin a halicci duniya.

***Ɗinbin mutane waɗanda basu da Ceto tukunna Waɗanda kuma Allah ba zai iya Hallakawa ba.***

A yau, akwai ɗinbin mutane a duniya waɗanda har yanzu basu sami ceto ba amma kuma Allah ba zai iya horonsu sabili da zunubansu ba. Ta yaya aka yi haka?

Wannan ya faru ne kasancewa Allah ya rigaya ya zaɓi waɗannan domin samun ceto. Sabili da haka tun kafin a haifesu, an rigaya an ɗibiya dukan munanan zunuban da waɗannan zaɓaɓɓun zasu aikata a bisan Ubangiji Yesu Kristi a matsayin madadin su, mai tsaya musu, wanda ya tsaya a gaban dakalin shari'ar Allah a madadinsu. Kuma sabili da zunubansu ne Kristi ya zamo mai laifi a gaban shari'ar adalci ta Allah kuma Allah ya hore shi sabili da zunubansu.

Sabili da haka waɗannan mutanen da Kristi ya ɗanɗana hukumcin Allah a madadinsu yanzu sun zama baratattu. Wato, an cika dukan abin da shari'ar Allah ta nema game da zunubansu kome muninsa. Waɗannan mutanen sun zama masu adalci.

Sabili da haka, yayinda ake haihuwar mutanen nan a cikin wannan duniya, a tabbace yake cewa ba zasu taɓa ɗanɗana hukuncin Allah domin zunubansu ba. A maimakon haka, a wani matsayi cikin rayuwarsu, a tabbace yake cewa Allah zai shimfiɗa kalmarsa, Littafi Mai-Tsarki, a cikin rayuwarsu, kuma zasu karɓi sabon rayayyen ruhu. Wannan na iya faruwa a duk lokacin da Allah ya zaɓa ya faru. Zai iya faruwa lokacin da suke cikin cikin uwarsu ko kuma 'yan mintoci kaɗan kafin su mutu. Zai iya faruwa ko suna da taɓin hankali ko kuma suna cikin hankalinsu. An baratas da waɗannnan mutanen tun kafin a haife su.

| *Zai iya faruwa lokacin da suke cikin cikin uwarsu ko kuma 'yan mintoci kaɗan kafin su mutu* |
|---|

Sai dai kuma ba wanda ya san ko su wanene mutanen nan sai dai Allah. Sai bayan sun karɓi sababbin ruhohinsu, wato, bayan sun zama cetattu, kafin su fara gane cewa Allah ya cece su. Amma gaskiyar ita ce, an barataddasu tun fil'azal domin Kristi shine Ɗan Ragon da aka yi hadaya dashi tun kafuwar duniya (Ruya ta Yohanna 13:8)

Sai dai kuma idan suka sami ceton, zasu san sun sami ceto ne domin a cikin alherinsa, Allah ya zaɓe su ya kuma biya bashin zunubansu. A kuma lokacin da Allah yake cetonsu yake kuma basu sabon rayayyen ruhu na har abada, ceto yakan zama tabbatacce a cikin rayuwarsu.

Ta haka, a cikin wannan lokaci a tarihi, akwai ɗinbin mutane waɗanda suke rayuwa cikin zunubi kamar yadda sauran duniya ke rayuwa cikin zunubi, amma kuma ba zasu shiga wani hukumci sabili da zunubansu ba.

*Cikin Yanayin Mutumtaka, Dukan Mutane Matattu ne a Ruhaniya*

Dole ne mu sani cewa kowane mutum, ko zaɓaɓɓe na Allah domin ceto ko ba wanda Allah ya zaɓa domin ya ceta ba, matacce ne cikin ruhaniya. Zunubi ya dabaibaye su jiki da ruhu. Shi ya sa Matta 15:19 ta ce:

**Gama daga cikin zuciya miyagun tunani ke fitowa, kisankai, zina, fasikanci, sata, shaidar zur, alfasha.**

A cikin Afisawa 2:3 Allah ya bayyana rayuwar waɗanda ya zaɓa domin ya ceta kafin ya cece su da cewa:

**A cikinsu kuwa mu duka muna zamanmu a da, a cikin sha'awoyin jikinmu, muna bin gurin jiki da na tunani; bisa ga tabi'a kuma 'yan tawaye ne, kamar sauran mutane.**

*Bisa ga shari'ar adalcin Allah, dole ne a biya bashin zunubi, abin da dokar ta bukata domin wannan biyan kuwa shine hallaka.*

Dole ne a kowane lokaci mu riƙa tuna cewa bisa ga shari'ar adalci ta Allah, dole ne a biya bashin zunubi, abin da dokar ta bukata domin wannan biyan kuwa shine hallaka. Sai an gama wannan biyan kafin Allah ya bada rai, rai madauwami, ga mai zunubi. Kuma domin abin da dokar ta bukata na biyan shine hallaka, wanda bashi da ceto zai hallaka har abada, ba kuma zai ƙara rayuwa ba. Allah ya bayyana wannan hallakar a cikin Ruya ta Yohanna 10:14-15 inda ya ce:

**Ni ne makiyayi mai-kyau; na san nawa, nawa kuma sun san ni, kamar yadda Uba ya san ni, ni kuma na san Uba; ina kuwa bada raina domin tumakin**

Kuma mutuwa da jahannama an jefar da su a tafkin wuta, wannan ita ce mutuwa ta biyu. Kuma duk wanda aka samu baya rubuce a cikin wannan littafin rayuwa an jefar dashi a tafkin wuta.

Da zaran an jefa mutum cikin ƙorama ta wuta, to an gama da shi kenan, an hallaka shi kenan har abada. Ba yadda zai yi ya sake rayuwa kuma. Wannan shine jigon "Mutuwa ta biyu".

Sai dai kuma, tun kafin a haife shi, Kristi ya rigaya ya biya bashin zunubin dukan zaɓaɓɓu, sabili da haka, mutumin ya zama baratacce (wato, bisa ga doka, yanzu bashi da wani laifi kuma). Amma kafin Allah ya shinfiɗa masa Maganar Allah ya kuma bashi rayayyen ruhu, mutumin nan yana rayuwa ne ƙarƙashin fushin Allah. Wato, har a kafin wannan lokacin, yana ɗauke da harbin zunubi, kuma har a wannan lokacin, shi matacce ne a ruhu. Yana wari kamar ruɓaɓɓar gawa (Yohanna 11:39) kamar kwarin busassun ƙasusuwa kuma (Ezekiel 37:1-2). Ba shi da wata hanyar canza yanayinsa na matacce a ruhu kamar yadda mutumin da ya mutu bashi iya mai da kansa ya zama mai-rai kuma.

### *Dole ne a Bamu Sabon Ruhu*

Kamar yadda muke gani a lokacin haihuwar jariri, Allah ne kaɗai ke iya bada rai. Ba wata gudumuwar da wannan yaron zai iya bayaswa domin ya sami rai na wannan jikin. Haka kuma, ko da yake Kristi ya rigaya ya biya bashin zunuban sa, dole ne sai an ba dukan wanda Allah ya zaɓa domin ya ceta rai na ruhaniya. A cikin Yohanna sura 3 aya 7, Allah yayi magana a kan wannan ya kuma kira shi "Maya haihuwa." Kalmar Helinancin da Allah yayi amfani da ita anan tana nufin "haihuwa daga bisa." Haka kuma a 1 Bitrus 1:23, Allah ya nanata cewa wannan sabuwar haihuwar ita ce "maya haihuwa."

Wannan sabuwar haihuwar wadda ke fitowa daga bisa, wato, daga sama, ba wai ƙwayar iri na rai da a kwana a tashi zai yi girma a cikin rayuwar wanda aka ceta ɗin ba ne. Sabon ruhu

ne wanda ke shiga nan take. Irin shine Kristi da kansa wanda yake zaune a cikin mutumin (Yohanna 14:23). Yayinda Allah yake yin amfani da misalin yin amfani da sabon ƙyalle domin a yi facin tsohuwar taguwa (Matta 9:16). Dole ne taguwar ta zama sabuwa gaba ɗayanta. Haka kuma, ya bada misalin ƙoƙarin zuba sabon ruwan inabi a tsofaffin salkuna. Dole ne a sa ruwan inabin a sababbin sulkunan (Matta 9:17). An nanata wannan a cikin waɗansu nasoshin Littafi Mai-Tsarki kamar su 2 Korantiyawa 5:17 inda muka karanta cewa:

**Idan fa kowane mutum yana cikin Kristi, sabon halitta ne: tsofaffin al'amura sun shuɗe, ga kwa sun zama sabobi**

Sashen yanayin mutum da nan take yake zamowa sabon halitta shine ruhu (sabon rayayyen ruhu), wanda Allah yake bashi a daidai lokacin da yake shinfiɗa Maganar Allah a cikin rayuwarsa (Ezekiel 36:26). Haka kuma a ƙarshen zamani, wannan zaɓaɓɓen zai karɓi sabon rayayyen jiki, "Farat ɗaya, da ƙyaftawar ido, da ƙarar ƙaho na ƙarshe: gama ƙaho za shi yi ƙara, matatttu kuma zasu tashi marasa-ruɓuwa, mu kuma za mu sake." (1 Korantiyawa 15:52).

Ta haka, an bada muhimman misalai a cikin Littafi Mai-Tsarki waɗanda ke nuna rashin iyawar mutum ya maida kansa rayayye a cikin ruhu, wato, ya sami ceto. An ƙarfafa wannan a cikin Ezekiel 37, inda Allah ya kwatanta mutane da busassun ƙasusuwa, amma kuma Allah ya nuna cewa lokacin da Allah yayi aikinsa, waɗannan busassun ƙasusuwan sun dawo rayayyu. Wani misali na tarihi kuma na rubuce a cikin Yohanna sura 11, inda muka ji labarin ruɓaɓɓar gawar Li'azaru ta fito daga kabari da rai bisa umurnin Ubangiji Yesu. Haka kuma, Allah ne kaɗai zai iya kawo rai madauwami na ruhaniya a cikin mutum wanda yake matacce a ruhu.

*Zamu iya tabbatas da cewa akwai mutane*
*marasa ceto iri biyu a duniya*

Zamu iya tabbar da cewa akwai mutane marasa ceto iri biyu a duniya. Akwai mutanen da suke matattu a ruhu waɗanda suke zaɓaɓɓu, waɗanda kuma a bisa shari'a, sun fita daga

ƙarƙashin fushin Allah, akwai kuma waɗanda basu cikin zaɓaɓɓun, sabili da haka, tabbatacce ne cewa ba zasu sami rai na har abada ba kuma zasu wahala a cikin fushin Allah na ƙarshe. Ko da shike dukansu biyu matattu ne cikin ruhaniya, duk da haka akwai dokar Allah a rubuce a cikin zukatansu. Sabili da haka, sun sani, kuma lamirin su yana shaida musu cewa ya kamata su yi biyayya da shari'ar Allah.

Haka kuma ruhu yana haɗe da yanayin su, Allah kuma yana amfani da ruhunsu domin ya jagorance su zuwa marmarin yin biyayya da dokokin Allah, ko kuma Shaiɗan ya jagorance su zuwa mugunta. Haka kuma, manne da yanayinsu, akwai mugunta, mutuwa ta ruhaniya wadda bata bukatar wani taimako daga Shaiɗan domin su bayyana cikin tunani, magana da ayyukan mutanen.

### *Tabbacin Ceton Zaɓaɓɓu*

Kamar yadda muka rigaya muka gani, akwai wani babban abu da ake bukata wanda kuma Allah ne da kansa zai yi. Mutanen da aka zaɓa domin a ceta, mutane masu zunubi. Basu san kome game da shirin Allah domin su ba. Dole ne sai an shinfiɗa ainihin shirin Allah domin cetonsu a cikin rayuwarsu.

Kafin mutum ya sami ceto, ba wani ɗan adam da ya sani ko Allah ya zaɓi ya cece shi ko babu. Sai bayan Allah ya cece mu kafin muke gane cewa iyakar dalilin da ya sa Allah ya haɗa mu a cikin shirinsa na ceto shine domin girmansa da kuma yana so ya zaɓe mu tun ma kafin ya halicci duniya. Cetattu na jiki ne da ruhu kamar waɗanda basu da ceto. Jikinsu yana ɗaya daga cikin yanayinsu wanda ake bizne wa sa'adda suka mutu. Ga wanda kuma yake da ceto, a lokacin da gangar jikin take mutuwa, ruhu (wanda shima yana cikin yanayin mutum) ya kan rabu da jiki a kuma ɗauke shi zuwa sama inda zai zauna ya kuma yi mulki tare da Kristi. Daga nan, a ƙarshen duniya, lokacin da Kristi zai dawo, zai tada jikin (2 Korantiyawa 5:8; 1 Tassalunikawa 4).

Sai dai kuma, kafin samun ceto, kowane zaɓaɓɓe yana rayuwarsa a wannan duniya kamar kowane mutum wanda ba'a zaɓa domin ceto ba.

A Afisawa 2:1-3 mun karanta wani abu game da zaɓaɓɓun cewa:

**Ku kuma ya rayad da ku, yayinda ku ke matattu ta wurin laifuffukan ku da zunubanku, inda ku ke tafiya a da bisa ga zamanin wannan duniya, ƙalƙashin sarkin ikon sararin sama, ruhun da ke aikawa yanzu a cikin 'ya'yan kangara; a cikinsu kwa mu duka muna zamanmu a da a cikin sha'awoyin jikinmu, muna bin gurin jiki da na tunani; bisa ga tabi'a kuma 'ya'yan fushi ne, kamar sauran mutane.**

Kafin ya sami ceto, yana marmarin zunubi a cikin jikinsa, a cikin ruhunsa kuma, yana sha'awar zunubi. Matacce ne shi cikin ruhaniya kamar kowane mutum wanda ba zai taɓa samun ceto ba.

Wannan shi ya kawo mu babban abu na uku wanda Allah ya aikata a madadin waɗanda Kristi ya zo domin ya ceta.

### *Mu'ujjuzar Sabuwar Haihuwa*

Aiki na uku da Allah yayi a madadin waɗanda aka baiwa Kristi a matsayin nasa har abada shine ya yi wani abin al'ajibi na ba zaɓaɓɓen sabon rayayyen ruhu. Yesu yayi magana akan wannan a Yohanna 3:5 inda yace:

**... Hakika, hakika ina ce maka, in ba a a haifi mutum daga cikin ruwa da Ruhu ba, ba shi da iko ya shiga cikin mulkin Allah ba.**

Kafin wannan, mun karanta a Yohanna 3:3 cewa:

**..... Hakika, hakika ina ce maka, im ba a haifi mutum daga bisa ba, ba shi da iko shi ga mulkin Allah ba.**

A haifi mutum da ruwa da kuma Ruhu shine, a haifi mutum daga Bishara (ruwa), ta wurin aikin Allah Ruhu Mai-Tsarki (Yohanna 4:10-15, Yohanna 7:38). Allah yayi magana akan wannan aikin a Romawa 10:17, inda ya ce:

**Bangaskiya fa daga wurin ji ne, ji kuma daga wurin maganar Kristi.**

A cikin shirin Allahntakar Allah, Ya shirya yanayi inda yake ceton mutane. Wannan yanayin shine Littafi Mai-Tsarki, wanda shi kaɗai ne Maganar Allah. Sabili da haka, bashi yiwuwa wani mutum ya sami ceto a cikin wannan duniya sai dai in sun ji maganar Allah, kuma Littafi Mai-Tsarki shi kaɗai ne maganar Allah. Shi yasa a zamanin ikklisiya aka yi ta ba majami'u dokar su watsa Bishara a cikin dukan duniya. Wannan shi ya sa muma ya kamata mu himmatu wajen watsa Bishara ga dukan duniya a wannan zamanin namu, amma yanzu muna yi ne a matsayin mutum ɗaya ɗaya, a maimakon a matsayin wata ƙungiya ta ikklisiya. Kowane ɗayanmu yana bauta a matsayin jakada na Kristi.

Ya kamata mu sani cewa yanzu ba wanda zai sami ceto a cikin ikklisiya. A bisa ga tsarin lokaci na Allah, zamanin ikklisiya ya rigaya ya wuce, kuma Ruhu Mai-Tsarki yayi watsi da ikklisiyoyi. Sai dai kuma, Littafi Mai-Tsarki ya umurce mu da cewa ana shigo da wani babban girbi na masu bi na gaskiya zuwa cikin mulkin Allah waje da ikklisiya. (Muna gayyatarka ka nemi Family Radio, ka nemi a baka kyautar littattafan nan, Ƙarshen zamanin ikklisiya da kuma abin da ya biyo baya, da Alkama da Zawan)

Allah ne ya gudanar da dukan aikin ceto, sabili da haka yana iya ceton mutum a kowane lokaci na rayuwar mutumin. Iyakar abin da ake bukata shine mutumin ya kasance mai sauraron Littafi Mai-Tsarki. A lokacin samun ceto, Allah yakan ba mutumin kunnuwa na ruhaniya da sabon ruhu madauwami. Kamar yadda muka gani a baya, jariri na iya samun ceto kamar yadda babba zai iya samu. Mutum mai tunani irin na yaro mai shekara biyu na iya samun ceto kamar yadda shehun malamin jami'a zai iya samu.

A bisan giciyen, lokacin da ya biya bashin zunuban dukan cetattu, Kristi ya nuna yadda ya sha wahala tun kafin kafawar duniya. Iyakar abin da ya rage shine a wani lokaci wanda Allah ne kaɗai ya sani, Allah zai sa mutumin ya ɗanɗana tabbacin ceto.

Har ya zuwa wannan lokacin na binciken mu, mun fara koyon abin da dokar Allah, Littafi Mai-Tsarki ya bukaci Allah yayi. Kila wannan tambayar: Me zan yi domin in sami ceto, zata yi ta bugawa a cikin tunaninmu. Shin ko akwai wata hanya wadda zan iya tabbatarwa ko ina cikin waɗanda aka zaɓa domin a ceta? Zamu yi ƙoƙari mu amsa wannan babbar tambaya a cikin binciken mu.

### *Fasarar da Littafi Mai-Tsarki ya ba Aiki na Ruhaniya*

A wannan matakin na bincikenmu, zamu gabatar da al'amari wanda ya bada nauyi ga maganar samun ceto. Wannan kuwa ya shafi fasarar da Littafi Mai-Tsarki take da shi na "aikin" ruhaniya. Littafi Mai-Tsarki yayi ta nanata cewa ceton mu ba zai taba zama sakamakon wani aiki da muka yi ba (Afisawa 2:8-9; Galatiyawa 2:16). Sabili da haka, dole ne mu san ma'anar da "aiki" yake da ita a gaban Allah.

A cikin Yunana 3:10 Allah ya ce:

**Allah kuwa ya ga ayyukansu, da suka juya ga barin mugun tafarkinsu; Allah kwa ya tuba ga barin masifar da ya ce za ya yi musu; bai kuwa aikata ba.**

A Matta 7:22 Allah ya ce:

**A cikin wannan rana mutane da yawa zasu ce mani, Ubangiji, Ubangiji, ba mu yi annabci da sunnanka ba, da sunanka kuma muka fitarda aljannu, da sunnanka kuma muka yi ayyuka da yawa masu iko?**

| *A duk lokacin da muka yi biyayya da dokar Allah, muna yin aiki wanda ke farantawa Allah rai.* |
|---|

Daga waɗannan ayoyin na Littafi Mai-Tsarki, mun koyi cewa a duk lokacin da muka yi biyayya da dokar Allah, muna yin aiki wanda ke farantawa Allah rai. Lokacin da muke rashin biyayya da dokar Allah, muna aikata abin da ke ɓatawa Allah rai. A misali, Littafi Mai-Tsarki ya umurci dukan mutane da su gaskanta da Krsiti. Shin gaskantawa aiki ne da muke yi? Hakika

aiki ne. Gaskantawa da bangaskiya abu ɗaya ne. A cikin 1 Tassolunikawa 1:3 da 2 Tassolunikawa 1:11 Allah yayi magana akan "aikin bangaskiya."

A cikin 1 Tassolunikawa 1:3 Littafi Mai-Tsarki ya ce:

**Babu fashi muna tuna da aikin bangaskiyarku da ɗawainiyar ƙamnarku da hanƙurin begenku cikin Ubangijinmu Yesu Kristi, a gaban Allahnmu Ubanmu**

A cikin 2 Tassolonikawa 1:11 kuma mun karanta cewa:

**Saboda wannan fa, kullum muna addu'a dominku, Allahnmu shi maishe ku ku cancanci kiranku, ya kuma biya kowane muradin nagarta da kowane aikin bangaskiya, bisa ga ikonsa.**

Allah yayi magana akan aikin bangaskiya da kuma ɗawainiyar ƙauna. Sabili da haka ya kamata mu gane cewa bangakiya da ƙauna duka ayyuka ne da muke aikatawa. Haka kuma, yin biyayya da dokokin Littafi Mai-Tsarki aiki ne da aka umurcemu mu yi. Sabili da haka ya kamata mu riƙe a zukatanmu cewa yayinda Allah yake umurtarmu mu yi addu'a, mu nemi Kristi, mu sami ceto, mu kira bisa ga sunan Allah, mu dogara ga Allah, mu karanta mu kuma bincike Littafi Mai-Tsarki da dai sauransu, a cikin dukan waɗannan umurnin, Allah yana umurtarmu da mu yi aiki. A misali, Wannan shi ya sa Allah ya kira "ƙauna" kiyaye dokar Allah. Yayinda muke ƙaunar Allah muke kuma ƙaunar maƙwabtanmu, muna aiki na ruhaniya. Wannan ƙa'idar da ke cewa yin biyayya da kowace irin doka, aiki ne da muke yi, ƙa'ida ce mai muhimmanci da bai kamata mu manta da ita ba a duk lokacin da muke binciken ayoyin Littafi Mai-Tsarki waɗanda suke da dangantaka da samun ceto.

*Kristi yayi Dukan Ayyukan da ake Bukata Domin Ceton mu*

Akwai kuma wata muhimmiyar ƙa'ida da ta zama dole a kowane lokaci mu riƙa tunawa. Wannan ƙa'ida ita ce Allah ne kaɗai ke iya yin aikin da ake bukata domin ceton wani mutum. Zaɓen waɗanda Allah ya shirya ya ceta, biyan bashin da Kristi yayi a madadin waɗanda ya zo domin ya ceta, sabon ruhun da

Allah yake ba waɗanda ya ceta: dukan waɗannan ayyuka ne da Allah kaɗai ke iya yi.

| *Allah ne kaɗai ke iya yin aikin da ake bukata domin ceton wani mutum* |
|---|

Gaskiyar ma ita ce, an yi zaɓen ta kafin a halicci wani mutum. Bugu da ƙari kuma, an gama biyan bashin zunuban zaɓaɓɓun tun kafin kafuwar duniya (Ruya ta Yohanna 13:8). Sabili da haka ba shi yiwuwa wani mutum ya iya yin wani abu domin taimakawa wajen samun ceto.

### *To menene ya sa Allah ya Bamu Waɗannan Dokokin?*

Allah ya bamu waɗannan dokokin domin mu gaskanta, mu yi addu'a, da dai sauransu, amma ta yaya ma zamu iya fara kiyaye waɗannan dokokin? Mu matattu ne ta ruhaniya. Allah ya kwatanta mutanen da basu da ceto da kwarin busassun ƙasusuwa (Ezekiel 37:1-14) da kuma gawa mai wari (Yohanna 11:39). A cikin Romawa 3:10-12 kuma, Allah ya nanata cewa:

**Kamar yadda an rubuta, Babu mai adalci, ko ɗaya, babu mai fahimta, babu mai neman Allah; Dukansu sun ratse sun zama marasa amfani baki ɗaya; babu wani mai aikata nagarta, babu ko guda ɗaya.**

Hakika Littafi Mai-Tsarki ya nanata mutuwar mutum wanda bashi da ceto. Ya kamata mu tuna cewa mutum, faro daga faɗuwar Adamu, ya mutu a cikin ruhaniya domin Allah ba ya rayuwa a cikinsa, kuma baya samun ƙarfinsa daga Allah. Sabili da zunuban mutum kuma, mutum ya kasance a ƙarƙashin fushin Allah, wannan kuwa yana nufin za'a hallaka shi a ƙarshen duniya ba kuwa zai ƙara rayuwa ba. Kamar yadda muka gani a baya, a cikin yanayinsa, mutum ya ƙazamtu da zunubi.

Sai dai kuma, ko da yake mutum ya zama matacce a ruhaniya, zai iya yin biyayya da dokokin Allah har ya zuwa wani mataki. Sabili da haka, zamu iya gaskantawa da Kristi har ya zuwa wani mataki, zai iya yin addu'a, zai iya neman Allah, kuma

zai iya gujewa waɗansu zunubai kamar su shan giya, ƙarya da sauransu. Zai iya yin haka domin a ƙalla dalilai biyu.

Dalili na farko shine har yanzu yana da lamiri wanda ke nanata masa zunubi (Romawa 2:14-15, Yohanna 8:9). Wannan ya faru haka domin an halici mutum a sifar Allah, don haka ko da shike mutum ya zama bara ga Allah, har yanzu akwai ɗan sauran dokar Allah a cikin lamirinsa.

Dalili na biyu shine Allah zai iya aikata abin da yayi niyya a cikin rayuwar wanda bashi da ceto ko da Allah bai yi niyyar cetonsa ba. Mun ga wannan ya faru a cikin rayuwar Balaam (Littafin Lissafi 22:12-13) da kuma cikin rayuwar Saul, sarkin Isra'ila na farko ( 1 Samu'ila 10:9-12).

Haka kuma, idan Allah ya zaɓi mutumin da bashi da ceto ya kuma biya dukan bashin zunubansa, kafin Allah ya bashi sabuwar zuciya, sabon rayayyen ruhu, ba wuya Allah Uba yana jawo shi (Yohanna 6:44).

Sai dai kuma, yayinda wannan mutumin yake iyakacin ƙoƙarinsa ya yi biyayya da dokokin Allah, ba zai iya sanin ko wanne dalili ba ne ke janshi zuwa yin biyayya da dokokin Allah. Wato, bashi da wata shaida, kuma ba zai yi tunanin cewa yin biyayyar shi ita ce shaidar yana da ceto ba.

### *Dangantakar Allah Mai ɗaurin kai da Mutum*

Har wayau, akwai wata dangantaka ta ƙut da ƙut wadda ta wuce gaban ganewa tsakanin Allah da kowane mutum. Wannan kuwa ba tsakanin Allah da mutumin da ya zaɓa domin ya ceta kaɗai ba, amma haka yake har tsakanin Allah da mutanen da bai zaɓa ya ceta ba, sabili da haka a ƙarshe dole za a hallaka su.

Mun ga wannan a sa'ad da Yesu yake zubar da hawaye sabili da Urshalima (Luka 19:41), wannan ya faru duk da cewar Littafi Mai-Tsarki ya bada shaida a fili cewa za a lalata Urshaliman nan da Yesu yake fuskanta. Mun kuma ga wannan a inda Littafi Mai-Tsarki ke shaida cewa Allah baya jin daɗin mutuwar mugu (Ezekiel 33:11). Mun ga wannan a gaskiyar cewa a cikin zuciyar kowane mutum, dokokin Allah suna nan a rubuce (Romawa 2:15).

Mun ga wannan a cikin dokar Allah mai cewa dole ne mutumin da ya kashe wani mutum wanda aka halitta a surar Allah ya mutu (Farawa 9:6). Mun ga wannan a umurnin Allah cewa mu ƙaunaci maƙiyanmu. Mu tuna cewa kowane mutumin da ba zaɓaɓɓe ba abokin gaban Allah ne, amma kuma ba mutumin da ba zamu ƙaunata ba. Mun ga wannan a cikin kashedin da Yesu ya bayar a Matta 5:22 cewa kada mu kira kowa "Raca" wato watsatse ko wawa. Ba mutumin da ke da rai da zamu duba a matsayin marar begen samun ceto.

Daga waɗannan shaidun zamu iya cewa ko da yake mutum ya zama matacce ta ruhaniya, kuma bashi samun ƙarfi ko kasancewar Allah a cikinsa, ba a zubar da shi ko raba shi da Allah ƙwataƙwata ba. A cikin kasancewarsa matacce a ruhaniya, har yanzu yana da alhakin yiwa Allah biyayya, haka kuma, yana iya yiwa Allah biyayya. Sai a rana ta ƙarshe ne za'a raba shi da Allah kwatakwata (Ishaya 66:24, Irmiya 23:39-40, 24:10).

Sabili da haka Allah zai iya bukatar kowane mutum da ya yi aikin gaskantawa da Allah domin su iya yin biyayya da umurnan Littafi Mai-Tsarki. Kamar yadda muka gani a binciken mu na baya, Allah zai iya zuga mutum yayi wannan biyayyar ta wurin yin aiki a cikin rayuwar wannan mutumin kamar yadda ya faru ga mugun mutumin nan Balaam (Littafin Lissafi sura 22 aya 23), ko kuma Allah yana iya aiki a rayuwar mutumin da yake zaɓaɓɓe na Allah sai dai kuma bai rigaya ya karɓi sabon ruhu ba tukuna (Yohanna 6:44).

## *Allah yana da ikon ya umurci 'yan adam suyi masa biyayya*

Dole ne mu tuna cewa Allah yana da iko ya umurci 'yan adam suyi biyayya da dokokinsa. Domin an halicci mutum a cikin sura da kuma kamanin Allah, dukan mutane kamar Allah da kansa, suna ƙarƙashin littafin shari'ar Allah, wato Littafi Mai-Tsarki. Sabili da haka ya kamata mu gane cewa za'a iya ganin aikin gaskantawa da Kristi a cikin mutumin da bashi da ceto wanda kila nan gaba ya sami ceto ko kuma ba zai sami ceto ba ma sam sam. Yayinda yake gaskantawa da Kristi, zai yi ƙoƙari yayi biyayya da dokar nan dake cikin Littafi Mai-Tsarki a Luka 13:24 inda Allah ya ce,

**Ku yi ƙoƙari ku shiga ta matsatsiyar kofa: gama ina ce maku, mutane da yawa za su so su shiga, ba za su iya ba.**

Haka kuma a Ibraniyawa 4:11 mun karanta cewa:

**Mu yi anniya fa mu shiga cikin wannan hutu, kada kowane mutum ya faɗi bisa wannan misalin kangara**

Sai dai kuma dole mu nanata cewa babu wani aiki daga cikin ayyukan nan da zai tabbatas ko kuma ya taimaka wajen samun ceto domin dukan ayyukan da ake bukata na samun ceto sun rigaya sun kammala a cikin Kristi tun kafin a haifi mutumin.

> *Babu wani aiki daga cikin ayyukan nan da zai tabbatas ko kuma ya taimaka wajen samun ceto domin dukan ayyukan da ake bukata domin samun ceto sun rigaya sun kammala a cikin Kristi tun kafin a haifi mutumin*

Abin sha'awa shine, yayinda wanda bashi da ceto yake ƙoƙarin aikata nufin Allah, manyan albarku guda biyu sukan cika.

Albarka ta farko ita ce, yayinda marar ceton yake ƙoƙari yayi biyayya da dokokin Allah, zai zamar masa dole ya yi ta girma a sanin Littafi Mai-Tsarki. Yayinda yake koyon gaskiya kamar su munin zunubi, hukumcin zunubi, adalcin Allah da jinƙan Allah, wannan zai gina rayuwarsa.

Abu na biyu kuma shine, wannan zai kawo shi yanayin da zai sami zarafin jin maganar Allah. Ta haka, idan Allah yayi niyya ya cece shi, to yana a matakin da Allah zai shinfiɗa maganarsa a cikin zuciyar mutumin.

### *Allah Yana Gwada Mutum*

Akwai dalili na uku da yasa Allah ya umurci mutum da yayi aikin bangaskiya. Wannan yakan sa mutum a cikin gwaji ko jarabawa. Ko mutumin zai fara tunanin cewa wannan biyayyar da yake yiwa Allah zata taimaka masa wajen samun ceto?

A kowane lokaci Allah yana gwada mutum. An gwada Adamu da Hauwa'u a Gonar Adnin. Sun faɗi jarabawar sakamakon haka kuma zunubi ya shigo duniya. An jaraba

Ibrahim ta wurin umurtarsa da ya yi hadaya da ɗansa (Farawa 22). Bai faɗi jarabawar ba. An jaraba Isra'ilawa ta hanyoyi dabam dabam a cikin shekaru 40 da suka yi suna yawo a jeji. Sun faɗi jarabawar. Ana jaraba mai bi na gaskiya a kowace rana domin har yanzu yana cikin jiki wanda yake marmarin aikata zunubi. Allah ya jaraba Yesu ta wurin barin Shaiɗan ya jaraba shi. Bai faɗi jarabawar ba.

Haka kuma, umurnin yin aikin bangaskiya da kuma aikin kiran Allah domin ceto duk jarabawa ce. Ko zamu iya gane cewa ko da yake waɗannan dokoki ne daga Allah, dole ne kuma a yi biyayya da su, yin biyayya da waɗannan dokokin ba zasu taɓa iya zama sanadin ceton mu ba?

Wannan shirin na gwaji yana da muhimminci. A cikin yanayin mutum, mutum mai fahariya ne, kuma a kowane lokaci yana ƙoƙari ya yi wani abu domin samun yabo.

Haka kuma, akwai mutane da yawa, kila ma ba tare da sun san abin da suke yi ba, da basu yarda Allah zai cece su ba sai dai idan sun yi wani abu domin kansu.

*Kada mu yi tunani ko kusa da cewar wani aiki da muka yi zai iya taimakawa ko ta wata ƙanƙanuwar hanya wajen samo mana ceto.*

Amma Allah mai kishi ne. Allah yayi dukan aikin ceton mu. Sabili da haka bai kamata mu yi tunani ko kusa da cewar wani aiki da muka yi zai iya taimakawa ko ta wata ƙanƙanuwar hanya wajen samo mana ceto ba.

### *Babban Muhimmancin Ranar Asabaci ta Kwana na Bakwai*

A cikin Tsohon Alkawali an nuna wannan gaskiyar ta hanyoyi dabam dabam. Mu tuna cewa dole ne jama'a wato Isra'ilawa su kiyaye ranar Asabaci. Wata doka ce ta al'ada wadda ke nuna gaskiyar cewa Allah ne yake aikata dukan ayyuka na ceto. Kamar yadda Isra'ila ba zasu yi wani aiki ba kome ƙanƙantarsa a ranar Asabaci, haka kuma muma ba zamu iya yin wani aiki domin samun ceto ba. A cikin Fitowa 31:13-14 Allah ya ce:

**Ka yi magana da 'ya'yan Isra'ila, cewa, lallai za ku kiyaye sabbatai na: gama alama ce tsakani na da ku cikin dukan tsararakin ku: domin ku sani nine Ubangiji wanda ke tsarkake ku. Za ku fa kiyaye assabbat: gama mai-tsarki ne a gareku: dukan wanda ya ƙazamtadda shi hakika kashe shi za a yi: gama dukan wanda ya yi aiki cikinsa, za a datse wannan rai daga cikin mutanensa.**

A cikin waɗannan ayoyin, Allah yana kafa babban muhimmiyar shaidar nan ta cewa Allah ya rigaya ya gama dukan aikin tsarkakemu. Kalmar nan "tsarkakewa" na nufin keɓewa domin aikin Allah. Yayinda muka sami ceto. Ana keɓe mu cikin ruhaniya domin hidimarsa. A cikin wannan nassin, Allah yana nanata cewa shi ne yayi dukan aikin da ake bukata domin tsarkakewa ko kuma ceton mu.

A matsayin wata alama wadda take nuna wannan muhimmiyar koyarwar, Allah ya umurta cewa kada ayi wani aiki a ranar Asabaci. Dukan wanda yayi aiki a ranar Asabaci yana kama da wanda yake gaskanta cewa aikin ruhaniyar sa ne ya taimaka wajen samun cetonsa. Za'a hallaka irin wannan mutumin, wato har yanzu wannan mutumin zai ɗanɗana fushin Allah.

Allah ya bamu misali domin ya nuna muhimmancin wannan gaskiyar. A cikin Lissafi sura 15 aya 32-36, Allah ya bamu labarin wani mutum wanda ya ɗebi ƙirare a ranar Asabaci. Wannan wani ɗan ƙaramin abu ne na karyar dokar Allah game da yin aiki ranar Asabaci.

Amma lokacin da Musa ya tambayi Allah irin hukumcin da za a bayar domin wannan ɗan ƙaramin laifin, Allah ya umurta cewa a jejjefi mutumin nan da duwatsu har sai ya mutu. Wannan abin ya nuna muhimmancin da wannan gaskiyar take da shi na cewa dole ne mu gane cewa ceto yana samuwa ne ta wurin aikin Kristi shi kaɗai.

***BABU WANI JINKAI DOMIN WAƊANDA SUKE TUNANIN CEWA ZA SU IYA YIN WANI AIKI DA ZAI TAIMAKA MUSU SU SAMI CETO***

Kada muyi tunanin cewa muna taimakawa ga samun ceton mu ta wurin yin biyayya da dokar Allah. Mu tuna cewa

dukan biyayyar da zamu yi ga wata dokar Allah, aiki ne na ruhaniya da muke yi. Ta wurin hallaka mutumin nan da ya tara ƙirare ranar Asabaci, Allah yana yi mana shelar cewa: BABU WANI JINKAI DOMIN WAƊANDA SUKE TUNANIN CEWA ZA SU IYA YIN WANI AIKI DA ZAI TAIMAKA MUSU SU SAMI CETO.

*Albarkar da ke Cikin Shirin Gwaji na Allah*

Wannan shiri na gwajin babbar albarka ce ga waɗanda suka gaskanta cewa sun sami ceto. A Korantiya ta biyu (2) 13:5, Allah ya umurce mu da cewa:

**Ku gwada kanku ko kuna cikin imani; ku yi wa kanku ƙwanƙwanto. Ko ba ku sani ba ku da kanku, Yesu Kristi yana cikinku in dai ba yasassu ba ne ku?**

Ta yaya zamu iya tabbatar wa kanmu cewa mu cetattu ne na gaskiya? Ɗaya daga cikin manya manyan hanyoyin shine mu gwada yadda muka gaskanta cewa mun sami ceto.

Ya kamata mu tabbatar cewa mun kawar da dukan wani ra'ayi ko tunani wanda muke da shi wanda ke nuna cewa wannan abin ko wancan abin da muka yi shine ya taimaka mana muka sami ceto. Dole ne mu tabbatar da cewa muna riƙe da koyaswar Littafi Mai-Tarki mai cewa idan har mun sami ceto, Kristi ne yayi dukan aikin ceto tun kafin a haife mu. Kristi ne yake yin dukan aiki na ceto kuma babu abin da zamu yi domin mu taimaka wajen samun ceton mu. Dole ne mu gane cewa babu wani aiki, wato yin wata biyayya da dokar Allah da zata taimaka mana wajen samun ceto. Ya kamata hukumcin da ya faɗa kan mutumin da yake tara ƙiraren itace a ranar Asabaci ya zauna a cikin tunanin mu.

Haka kuma, muna jaraba kanmu ta wurin kalmomin 1 Yohanna 2:3-6, inda muka karanta cewa:

**Ta wurin wannan mun sani mun san shi, idan muna kiyaye dokokinsa. Wanda ya ce, Na san shi, amma ba ya kiyaye dokokinsa ba, maƙaryaci ne, gaskiya kwa ba ta cikinsa ba: amma wanda yana kiyaye maganatasa, a cikinsa lallai ƙaunar Allah ta cika. Domin wannan mun sani muna cikinsa: wanda ya ce yana**

**zamne cikinsa ya kamata shi da kansa ya yi tafiya kamar yadda shi ya yi tafiya.**

A kan bada sabon rayayyen ruhu ga dukan wanda ya sami ceto na gaskiya, sabili da haka, a kowane lokaci zai zama da farin cikin aikata nufin Allah. Kamar yadda mai Zabura ya faɗa a Zabura 139:23-24, zai yi addu'a:

**Ka yi bincike na, ya Ubangiji, ka san zuciyata. Ka auna ni, ka san tunanina: ka duba ko da wata hanyar mugunta daga cikina. Ka bishe ni cikin tafarki na har abada.**

*Allah yana Kara Tsananta Shirinsa na Gwaji*

Gwajin da waɗannan dokokin suke kawowa yana ƙara tsanani domin ko da yake mutumin da bashi da ceto matacce ne cikin ruhaniya kuma yana ƙarƙashin fushin Allah, duk da haka yana a matsayin da zai iya yin biyayya da dokokin Allah har ya zuwa wani mataki. A farkon wannan binciken mun koyi abubuwa kamar haka:

1. Mutumin da bashi da ceto yana da lamirin da ke nuna masa zunubi. Wannan ya faru ne kuwa domin akwai 'yan dokokin Allah rubuce a cikin zuciyarsa (Yohanna 8:9; Romawa 2:14-15).

2. Allah zai iya sa mutumin dake matacce a ruhu, a misali Balaam da Sarki Saul a cikin Tsohon Alkawali, ya aikata nufin Allah ko da ma Allah bai yi niyyar ceton wannan mutumin ba (Lissafi 22:12-13; 2 Bitrus 2:15-16; 1 Samu'ila 10:9-12; 1 Labarbaru 10:13).

Sabili da haka, koda shike mutum yana iyakacin ƙoƙarinsa yayi biyayya da maganar Allah, ba zai iya sanin ko Allah ne yake aiki a cikin zuciyarsa ko kuma lamirinsa ne yake kashe shi ba. Kuma ba zai iya sanin ko yana iyakacin ƙoƙarinsa domin yayi biyayya da Allah da dukan zuciyarsa ba. Amma dole mu sani cewa babu wani aiki na gamsar Ubangiji da zai iya sashi a hanyar samun ceto ko kuma da zai tabbatas masa da samun

ceto ko kuma wanda zai iya kai matsayin abin da ake bukata domin samun ceto.

| |
|---|
| *Yana kuma iya kuskuren yin tunanin cewa Allah zai cece shi domin yayi biyayya da waɗannan dokokin* |

Idan mutumin da bashi da ceto ya fara yin biyayya da dokokin Allah, zai iya faɗawa cikin tarkon yin tunanin cewa yin biyayyar sa shaida ce ta cewa Allah ya rigaya ya cece shi. Yana kuma iya kuskuren yin tunanin cewa Allah zai cece shi domin yayi biyayya da waɗannan dokokin. Cikin dukan waɗannan abubuwan, yana ƙetare dokar Allah ne mai cewa babu wani aikin da zai iya taimakawa mutum wajen samun ceto. Kuma ko da yake shirin Allah ne ya jaraba mutum ya ga ko mutum zai yarda yayi biyayya da dukan dokokin Allah, idan ba tare da jinƙan Allah ba, mutum zai faɗi wannan jarabawar.

Rayuwar Isra'ilawa ta nuna wannan sosai. Allah ya ce musu idan suka yi biyayya da dukan dokokinsa, zai albarkace su ƙwarai har abada (Kubawar Shari'a 28:1; 28:15; 30:6-16).

Sabili da haka sun yi ƙoƙari su yi abin da ya kamata, suna ganin cewa yin haka zai iya basu ceto. Sai dai kuma abin baƙin cikin shine a Romawa 9:31-32 Allah ya ce mana:

**Amma Isra'ila, cikin bin shari'ar adilci, ba su ruski shari'an nan ba. Don mi? Domin ba su neme ta bisa bangaskiya ba, amma kamar bisa ayyuka. Suka yi tuntuɓe wajen dutsen tuntuɓewa'**

Idan mutum yayi iyakacin ƙoƙarinsa ya sami ceto, ba wuya ya faɗi cikin tarkon yin tunanin cewa yin biyayya shine tushe, ko kuma zai iya bada ceto. Wannan yana kama da yin aiki a ranar Asabaci kamar mutumin nan da ya tsinci ƙiraren itace.

Ya kamata a kowace rana matsayinmu ya zama irin na mutanen Nineva, wanda kamar yadda muka karanta a littafin Yunana 3:9:

**Wa ya sani ko Allah za ya juya ya tuba, ya bar zafin fushinsa, kada mu lalace.**

| |
|---|
| *Ba zamu yi tunanin wai wani abu da muke ko kuma zamu yi* |

*zai taimaka ko kuma zai tabbatas da muna da ceto ba.*

Sabili da haka, ba zamu yi tunanin wai wani abu da muka yi ko kuma zamu yi zai taimaka ko kuma zai tabbatas da muna da ceto ba. Wannan gaskiyar kuma ta shafi ko mun gaskanta cewa Allah ne yake aiki a rayuwarmu domin mu aika nufinsa ko kuma muna ƙoƙari ne mu yi biyayya domin lamirin mu ya nuna mana cewa ya kamata muyi haka.

Dole ne addu'ar wanda bashi da ceto ta zama, "Ya Allah ka yi mani jinƙai. Ban cancanci samun ceto ba. Ina godiya domin yayinda nake ƙoƙarin aika nufinka, ina sane da cewar Allah ne kaɗai zai iya kai ni matsayin da zan nemi Allah da dukan zuciyata da dukan rai na, kuma wannan zai yiwu ne idan na sami sabuwar zuciya, wato lokacin da Allah ya cece ni kaɗai."

Ya kamata misalin mai karɓar harajin nan a cikin Luka 18:13 ya kasance a cikin tunanin mu. A wurin mun karanta cewa:

**Amma shi mai-karɓar harajin, da ya ke tsaye daga nesa ba ya yarda ya tada ko idanunsa sama, amma sai ya bugi ƙirjinsa ya ce, Ya Allah, ka yi mani jinƙai, ni mai zunubi.**

Ya kamata kuma mu tuna da kalmomin da Allah ya faɗa a Joel 2:12-14

**Amma ko yanzu in ji Ubangiji, ku juyo mani da dukan zuciyarku, tare da azumi da kuka da baƙin ciki: ku tsaga zukatan ku ba tufafinku ba, ku juyo wurin Ubangiji Allahnku: gama shi mai alheri ne, cike da juyayi, mai jinkirin fushi, mai yalwar jinƙai, yana sake nufinsa a kan masifan da ya shirya. Wa ya sani, ko ba za ya juya ya sake nufinsa ba, ya bar albarka a bayansa, watau hadaya ta gari da ta sha ga Ubangiji Allahnku?**

Ta wannan hanyar ne Allah yake jagorantar mutanensa, an kuma ƙara bayyana wannan a cikin Irmiya 31:8-9 inda muka karanta cewa:

**Duba! Daga ƙasar arewa zan kawo su, daga iyakar duniya zan tattaro su, tare da su kuma makafi da guragu, mace da ciki, da**

**mache mai wahalar haifuwa tare: babban taro hakanan za su dawo nan. Da kuka za su zo, da godo zan bishe su: zan kawo su bakin gulaben ruwaye, a cikin miƙaƙƙiyar hanya inda ba za su yi tuntube ba: gama uba ni ke ga Isra'ila, Ifraimu kuma ɗan fari na ne.**

***Zamu iya Sauraron Littafi Mai-Tsarki ba tare da Mun ji ba?***

Allah ya yi kashedi a wurare da dama cikin Littafi Mai-Tsarki, kamar yadda ya yi a cikin Irmiya 29:17-19, inda muka karanta cewa:

**In ji Ubangiji mai runduna: Ga shi, zan aike masu da takobi, da yunwa da aloba, in maishe su kamar munanan ɓaure, waɗanda ba su ciyuwa domin muninsu. Zan runtume su da takobi, da yunwa da aloba, in bashe su domin a yi shillo da su a cikin dukan mulkokin duniya, su zama abin la'ana, abin al'ajibi, abin reni, abin zargi, a cikin dukan al'ummai inda na kore su: don ba su kasa kunne ga zantattukana ba, in ji Ubangiji, waɗanda ina aike masu da su ta bakin bayi na annabawa, ina assubanci ina aikansu; amma kun ƙi ji, in ji Ubangiji.**

*Kasa kunne shine yin sauraro da niyyar fahimtar da kuma ƙoƙarin yin biyayya da abin da aka umurta*

Kasa kunne shine yin sauraro da niyyar fahimtar da kuma ƙoƙarin yin biyayya da abin da aka umurta. Sai dai kuma, mukan zo wurin Littafi Mai-Tsarki da wani ra'ayi da muke da shi na abin da muka gane da gaskiyar, ba zamu kasa kunne ga gaskiyar ba, sabili da haka, a bisa faɗar nassin nan, ba zamu ji gaskiyar Maganar ba.

A misali, mutumin da ya ke riƙe da wani mugun tunani, ko kuma ya yarda cewa irin bishararsa ta jeka-nayi-ka gaskiya ce, ko kuma wanda yake ƙetare dokar Allah ta ya nemi ceto da gangan, ba ya sauraron Maganar Allah. Da zaran ya karanta wani abu game da ceto a cikin Littafi Mai-Tsarki, sai ya juya maganar ko kuma yayi ƙoƙari ya ba maganar wata ma'ana da ta yi daidai da ra'ayin da yake da shi a cikin zuciyarsa. a gareshi, ra'ayinsa na tawaye ya kashe gaskiyar Littafi Mai-Tsarkin da ya

ji. Ya sa kansa a matsayin wurin da ba zai ji maganar Allah ba. Ta haka, ya sa kansa a wuri mai hatsari domin bangaskiya (Kristi a matsayin Mai ceto) na zuwa ne ta wurin sauraron Maganar Allah kaɗai (Romawa 10:17).

Gaskiya ne za'a iya tunanin cewa Allah yana iya ceton kowane mutum ba tare da yin la'akari da irin tayaswar da mutumin yake yiwa Allah ba, ko dama mutane sun taurare sunki su kasa kunne ga maganar Allah. Sai dai kuma, Littafi Mai-Tsarki bai goyi bayan waɗanda suke ƙin kasa kunne ga maganar Allah ba, sabili da haka, ya kamata mu yi tunani a kan gargaɗin da Irmiya 29:18-19 wanda muka karanta a baya yayi mana. Idan ka duba, irin wannan mutumin yana daidai da Ba-farisen nan da Matta sura 23 ta yi magana a kai..

Sai dai kuma, akwai hasken nasara, hasken nasara mai kyau, ga waɗanda suka yarda da zunubansu, waɗanda kuma suka juya ga rabuwa da ra'ayinsu, waɗanda suka ɗauki niyyar yin biyayya da dukan Littafi Mai-Tsarki, ga waɗanda kuma suke yin kuka ga Allah domin neman jinƙai.

> *Yayinda muke zuwa ga Littafi Mai-Tsarki, dole ne mu shiga cikinsa ba tare da wani ra'ayi na mu na kanmu ba, kome kyau ko kuma alamar ingancin ra'ayin*

Yayinda muke zuwa ga Littafi Mai-Tsarki, dole ne mu shiga cikinsa ba tare da wani ra'ayi na mu na kanmu ba, kome kyau ko kuma alamar ingancin ra'ayin. Dole ne mu kusanci Littafi Mai-Tsarki da tunanin "ban san kome ba. Ya Allah bari kai ka koya mani." Kuma yayinda muke ƙoƙarin yin biyayya da maganar Allah, bari ra'ayin mu ya zama bamu cancanci ceto ba ko kaɗan, amma muna da babban begen cewa kila Allah zai cece ni nima (Yunana 3:9).

### *Kwatanta Ayoyin Littafi Mai-Tsarki da Ayoyin Littafi Mai-Tsarki*

Dole ne mu tuna da wata babbar doka da dole ne a kiyaye, yayinda ake binciken Littafi Mai-Tsarki, wannan dokar kuma ita ce dole ne mu binciki Littafi Mai-Tsarki bisa ga ayoyin Littafi Mai-Tsarki (1 Korantiyawa 2:13). Wato, yayinda muke binciken Littafi Mai-Tsarki, dole ne mu tabbata cewa duk

matsayin da zamu ɗauka, yayi daidai da dukan Littafi Mai-Tsarki.

Riƙe wannan gaskiyar a cikin zuciyarmu, da kuma yin amfani da abubuwan da muka koya a wannan binciken, za mu dubi waɗansu ayoyi da suka yi magana game da samun ceto kai tsaye. Zamu fara da sananniyar ayan nan Romawa 10:13 inda Allah ya ce:

**Gama dukan wanda za ya kira bisa sunan Ubangiji za ya tsira.**

Nan da nan zamu gane cewa akwai wani abu da bai tafi daidai ba, wato, dole ne mu lura. Yin biyayya da dokar nan ta kira bisa sunan Ubangiji aiki ne da mukan yi. Da alamar wannan ayar tana cewa idan muka yi aiki na kiran sunan Ubangiji, wannan zai sa mu sami ceto, sai dai wannan bashi yiwuwa domin Allah yayi dukan aiki domin ceton mu. Sabili da haka, mun sani cewa ba zamu iya fahimtar wannan ayar ba tare da neman ƙarin bayani daga cikin Littafi Mai-Tsarki ba.

A cikin binciken mu na neman ƙarin bayyani, mun iso Irmiya 29:11-13 inda Allah yake cewa:

**Gama na san irin tunanin da ni ke tunaninku da su, in ji Ubangiji, tunani na lafiya, ba na masifa ba, domin in ba ku bege mai kyau a ƙarshe. Sa'annan za ku kira gareni, ku tafi ku yi mani addu'a, ni ma in ji ku. Za ku neme ni, ku same ni kuma, lokacin da ku ke nema na da zuciya ɗaya.**

An bayyana wannan gaskiyar a Kubawar Shari'a 4:29 inda muka karanta cewa:

**Amma idan daga can kun biɗi Ubangiji Allahnka, zaka same shi, idan ka biɗe shi da dukan zuciyarka da dukan ranka.**

Allah yana faɗa mana wani muhimmin abu cewa idan muna neman Allah domin ceto, dole ne mu neme shi da dukan zuciyarmu

Sai dai kuma wannan bashi yiwuwa domin Littafi Mai-Tsarki ya koya mana game da yanayin zuciyar mutumin da bashi da ceto. Mun karanta a Irmiya 17:9 cewa:

**Zuciya tafi komi rikici, cuta gareta ƙwarai irin ta fidda zuciya: wa za ya san ta?**

Mun kuma karanta a Markus 7:21 cewa:

**Gama daga ciki, daga cikin zuciyar mutum, miyagun tunani ke fitowa, fasikanci, sata, kisan kai, zina, ƙwaɗai, mugunta,**

| *kafin wani ya iya kira bisa ga sunan Allah da dukan zuciyarsa, dole ne sai an bashi sabuwar zuciya* |
|---|

Sabili da haka kafin wani ya iya kira bisa ga sunan Allah da dukan zuciyarsa, dole ne sai an bashi sabuwar zuciya, wato, sun rabu da muguwar zuciya. Abin da Littafi Mai-Tsarki ya koyas kuma ke nan, a misali, a cikin Ezekiel 36:25-27 Allah ya ce:

**Zan yayyafa muku ruwa mai tsabta, za ku tsabtata: daga cikin dukan ƙazamtarku da dukan gumakanku, zan tsarkake ku. Sabuwar zuciya kuma zan ba ku, sabon ruhu kuma zan sa a cikinku: daga cikin jikinku kuma zan amshe zuciyan nan ta dutse, in ba ku zuciya mai tabshi ta nama. In sa ruhuna a cikinku, in biyasda ku cikin farilaina, za ku kiyaye shari'u na, ku aikata**

A cikin waɗannan ayoyin, Allah ya koya mana a fili cewa Allah ne ke ba da sabuwar zuciya. Ta wurin babban abin al'ajibin nan na basu sabuwar zuciya wanda har yanzu akan kira sabon ruhu, zai sa mu yi tafiya cikin yin biyayya da shi. A cikin wannan binciken, mun kira sabuwar zuciya ko sabon ruhu sabon rayayyen ruhu, wanda mukan karɓa yayinda muka sami ceto. Ayoyin nan a cikin Ezekiel suna bayyana yadda Allah yake ceton mutum, wato, Allah ne kaɗai yake yin aikin ceton mu.

### *An Umurci dukan mutane da su Kira Bisa Sunan Ubangiji*

Mun karanta a Romawa 10:13 cewa "Gama Dukan wanda za ya kira bisa ga sunan Ubangiji za ya tsira," amma ba zamu ɗauki mataki game da ceto ba sai idan mun haɗa da ƙarin

hasken da muka samu cewa dole ne mu kira bisa ga sunan Allah da dukan zuciyarmu kafin mu sami ceto. Mun sani cewa kiran sunan Ubangiji haka kawai ba zai bada ceto ba. Kuma ba zamu iya kiransa da dukan zuciyarmu ba sai idan Allah ya rigaya ya cece mu ta wurin bamu sabuwar zuciya, wato, sai dai idan Allah ya rigaya ya yi dukan aikin cetonmu.

Sai dai kuma wannan ya shigo da wata sabuwar matsala. Romawa 10:13 ta furta cewa dukan wanda ya kira bisa ga sunan Ubangiji "za ya tsira." Waɗannan kalmomi "za ya tsira" kalmomi ne na Helinanci dake nuna cewa ceto wani abu ne da ke zuwa nan gaba sakamakon kira ga sunan Ubangijin da aka yi. Mun rigaya mun ga abin da Littafi Mai-Tsarki ke koyaswa a sashi na farko na wannan ayar da cewa dole ne mu kira bisa ga sunan Allah da dukan zuciya. Mun kuma koyi cewa zamu iya kiransa da dukan zuciya ne domin Allah ya cece mu, ya kuma bamu sabuwar zuciya kaɗai.

Sabili da haka da yake "za ya tsira" sakamakon kira bisa ga Allah da dukan zuciyarmu ne, muna da damuwa. Ta yaya za'a ceci mutumin da ya rigaya ya sami ceto?

Zamu iya warware wannan matsalar idan muka gane cewa mun rigaya mun koya a baya cikin wannan binciken cewa tabbacin ceto a cikin rayuwar wanda Allah ya zaɓa yana da matakai. Mataki na farko shine zaɓen mutumin da za a ceta. Mataki na biyu shine Kristi ya rigaya ya cika abin da Allah ya bukata game da zunubanmu, a daidai wannan lokacin ne, ya biya dukan hukumcin da ya kamata a ɗauka domin zunubanmu.

Mataki na uku na faruwa ne a lokacin da Allah yake ba zaɓaɓɓun, waɗanda Kristi ya ɗanɗana fushin Allah dominsu sabuwar zuciya ko sabon ruhu. Wannan matakin na uku shine yawancin lokaci muke magana akai yayinda muke magana akan samun ceto.

Amma har yanzu ceton mu bai zama cikakken ba. Har yanzu muna da jiki na zunubi da dole ne a ceta. Wannan shine ya kawo mu ga mataki na huɗu, wannan kuma zai faru ne a rana ta ƙarshe lokacin da Kristi za ya dawo ya ba dukan masu bi na gaskiya sababbin rayayyun jikuna (1 Korantiyawa 15).

Sabili da haka faɗin cewa "mun sami ceto," da kuma "zamu sami ceto" yayi daidai da abin da Littafi Mai-Tsarki ke koyaswa. Wannan shi ya sa a 1 Bitrus 1:5 muka karanta cewa:

**Ku da ke bisa ikon Allah kiyayayyu ta wurin bangaskiya zuwa ceto wanda yana nan a shirye ga bayanuwa a ƙarshen zamani.**

Shi ya sa kuma a Markus 13:13 muka karanta cewa:

**Za ku zama abin ƙi ga dukan mutane sabili da sunana: amma wanda ya jimre har matuƙa shi ne za ya tsira.**

| |
|---|
| *Kafin mu zama cetattu ta kowane fanni, sai a ƙarshe, lokacin da Allah zai bamu ɗaukakken rayayyen jiki.* |

Zamu jure har ƙarshe domin mun rigaya mun sami ceto. Amma Kafin mu zama cetattu ta kowane fanni, sai a ƙarshe, lokacin da Allah zai bamu ɗaukakken rayayyen jiki.

Ta haka, mun koya daga cikin waɗannan ayoyin cewa idan bamu yi biyayya da umurnin Littafi Mai-Tsarki mai cewa dole ne mu gwada abubuwa na ruhaniya da abubuwa na ruhaniya, zamu iya faɗawa a cikin tarkon da zai makamtar da mu daga ganin gaskiyar dake cikin Littafi Mai-Tsarki. Sabili da haka, bai kamata mu riƙe wani ra'ayi ba sai bayan mun bincike dukan Littafi Mai-Tsarki.

Har ya zuwa wannan lokaci, mun koyi waɗansu gaskiyoyi masu muhimmanci. Cikinsu kuwa akwai:

1. Kristi ne kaɗai yayi dukan aikin da ake bukata domin ceton wani mutum.

2. A dukan lokacin da muka kiyaye wata doka, muna yin aiki na ruhaniya ne. Ko da ma mutum bashi da ceto, zai iya aikata wani aiki na ruhaniya kamar su gaskantawa da Kristi, daidai gwargwado, sai dai wannan aikin ba zai iya zama sanadiyar cetonsa ko kuma ya taimaka masa wajen samun ceto ba.

Da waɗannan sharïɗun Littafi Mai-Tsarkin shinfiɗe a zukatanmu, an umurce mu cewa ɗaukar wai wata aya ta koyas da cewa samun ceton mu ya danganta ne da gaskantawa ko kuma kiyaye dokokin Littafi Mai-Tsarki ba daidai ba ne. Mun

sani cewa dole ne mu binciki Littafi Mai-Tsarki muyi addu'a domin hikima domin mu fahimci ayar da kyau.

*Aikin Gaskantawa*

Kalmar nan "gaskantawa" kusan ita ce kalmar da take bukatar a fahimta sosai yayinda ake magana akan ceto. Kamar yadda muka koya, kalmar nan "gaskatawa" ta fito ne daga kalmar nan "bangaskiya." Mun kuma rigaya mun koyi cewa bangaskiya aiki ne, sabili da haka, gaskatawa aiki ne na ruhaniya. Mun kuma koyi cewa babu wani aiki da zai kai mu ga samun ceto ko kuma da zai taimaka mana wajen samun ceto.

Maganar Allah na rubuce a cikin kowane mutum sabili da haka, mutum ko bashi da ceto zai iya yin aikin bangaskiya domin yana da lamiri. A gaskiya ma, yayinda mutum yake ƙoƙari domin ya shiga mulkin Allah, wato, ya sami ceto, zai yi biyayya da wannan dokar domin yana iya gaskantawa. Sai dai kuma irin wannan bangaskiyar ba irin bangaskiyar da ake dangantawa da ceto ba ce. A Romawa 10:9-10, Allah yayi magana akan waɗanda suke ceto suna gaskantawa daga zuciya. Ayoyin na cewa:

**Gama idan ka shaida da bakinka Yesu Ubangiji ne, ka kuma bada gaskiya cikin zuciyarka Allah ya tashe shi daga matattu, za ka tsira, gama da zuciya mutum yake bada gaskiya zuwa adilci, da baki kuma ake shaida zuwa ceto.**

Sai dai kuma mun koyi cewa zuciyar mutum cike take da mugunta (Irmiya 17:9; Matta 15:19). Domin haka, bashi yiwuwa mutum ya iya gaskantawa daga zuciya sai idan Allah ya bashi sabuwar zuciya. Idan kuma Allah ya bamu sabuwar zuciya, to wannan na nufin ya cece mu (Ezekiel 36:24-27). Sabili da haka, idan muka gaskanta kafin mu sami ceto, wannan gaskantawar ba daga zuciya take ba, domin haka ba za'a iya danganta ta da ceto ba.

Sai dai kuma, idan muka gaskanta da dukan zuciyarmu, wannan yana nufin cewa Allah ya rigaya ya cece mu ta wurin bamu sabuwar zuciya. Mun bada gaskiya ne domin Allah ya rigaya ya cece mu. Sabili da haka ba za'a ɗauki kalmar nan

"gaskantawa" da kuma "bada gaskiya" su zama wata hanya ta samun ceto ba.

Mun karanta a cikin Ayyukan Manzanni 8:13-23 cewa Siman mai sihiri ya gaskanta an kuma yi masa baftisma amma ayoyin da suka biyo baya sun nuna a fili cewa bai sami ceto ba. Ibrahim ya bada gaskiya domin Allah (Kristi) ne aka lissafta masa a matsayin adalci. Siman ya gaskanta a matsayin mutum wanda bashi da ceto. Ibrahim ya gaskanta a matsayin mutum wanda yake da ceto. Sai dai kuma bangaskiya bata taka wata rawa a cikin rayuwar Siman ko Ibrahim game da al'amarin ceto ba.

Sabili da haka zamu iya cewa yin aikin gaskantawa kafin mu sami ceto ba zai taɓa taimakawa wajen samun ceto ba ko kaɗan. Aikata aikin bangaskiya bayan mun sami ceto na faruwa ne domin Allah ya cece mu.

| |
|---|
| *Yin biyayya da dokar da ke cewa a gaskanta na da mawafuka da marmarin yin biyayya da dukan dokokin Allah.* |

Sai dai kuma, kalmar nan "bangaskiya" na nuna muhimmancin gaskantawa kafin a cece mu. Yin biyayya da dokar da ke cewa a gaskanta na da mawafuka da marmarin yin biyayya da dukan dokokin Allah. Waɗannan dokokin sun haɗa da ƙaunar Allah, neman ceto, dogaro gareshi, tuba daga zunuban, da yin addu'a domin ceto. Yin biyayya da waɗannan dokokin ayyuka ne waɗanda muke yi, sai dai ba zasu taɓa bamu ceto ba. Sai dai kuma irin wannan biyayyar zata samu mu riƙa sauraron Littafi Mai-Tsarki akai-akai kuma da lura. Ta yin haka, zamu kasance a cikin yanayin da ya dace domin samun ceto idan Allah ya shirya ya cece mu.

Ta yaya zamu gaskanta idan mu matattu ne a ruhu? Ka tuna, Allah ya kwatanta mutanen da basu da ceto da kwarin busassun ƙasusuwa (Ezekiel 37) da kuma kamar gawa mai wari (Yohanna 11:39). Allah ya furta cewa babu wanda yake neman Allah, babu ko ɗaya (Romawa 3). Waɗannan kalaman na nuna cewa kafin ceto, dukan mutane sun mutu, mutuwa ta ruhaniya. Ya mutu mutuwa ta jiki da ta ruhu, kuma Allah baya a cikinsa. Sabili da zunubansa, bisa ga shari'a, ya kasance ƙarƙashin fushin Allah kuma yana gangarawa zuwa hallaka.

Hukkumcin kowane zunubi hallaka ne, sabili da haka, idan ba Allah ya shiga tsakani ba, tabbas ne kowane mutum zai hallaka. Ko da yake shari'ar Allah tana cikin mutum har ya zuwa wani matsayi, kuma mutum yasan abin da ke daidai da abin da ba daidai ba domin yana da lamiri, duk da haka, idan ba tare da taimakon Allah ba, yanayin da yake ciki yanayi ne wanda babu wani bege. Sabili da haka yayinda mutumin da bashi da ceto yake aikata aikin gaskantawa da Kristi, duk da haka shi gawa ne mai wari, kwari na busassun ƙasusuwa. Ba zai iya neman Allah da dukan zuciyarsa ko kuma ya gaskanta da dukan zuciyarsa ba domin zuciyarsa cike take da mugunta. Sai dai idan Allah ya bashi sabuwar zuciya, wato, idan Allah ya cece shi ne kaɗai zai iya nema ya kuma gaskanta Allah da dukan zuciyarsa. Idan aka bashi sabuwar zuciya da sabon rahu, to ya zama rayayye na har abada.

**An Umurci Dukan Mutane da su Gaskanta da Allah**

Mun karanta a cikin Ayyukan Manzanni 16:31 cewa

**Suka ce, sai ka bada gakiya ga Ubangiji Yesu, za ka tsira, da kai da iyalin gidanka**

Mun sani cewa bangaskiya daga zuciya ne kaɗai yake da dangantaka da ceto. Kuma idan muka gaskanta daga zuciya, wannan ya nuna cewa mun rigaya mun sami ceto domin dole sai Allah ya bamu sabuwar zuciya kafin mu iya gaskantawa daga zuciya (Ezekiel 36:26). Sabuwar zuciya na nuna cewa mun sami ceto.

A cikin sanannar ayar nan ta Yohanna 3:16 mun karanta cewa:

**Gama Allah yayi ƙaunar duniya, har ya bada Ɗansa haifaffe shi kaɗai, domin dukan wanda yana bada gaskiya gareshi, kada ya lalace, amma ya sami rai na har abada.**

Mun sani cewa kalmomin nan "dukan wanda" ya shafi zaɓaɓɓu na Allah ne kaɗai. Mun kuma sani cewa mutumin da bashi da ceto wanda kuma Allah bai yi niyyar ceta ba yana iya gaskantawa da shi har na zuwa wani mataki. Kuma mun sani

cewa waɗanda suke samun ceto ba wai suna samun ceto domin sun yi aikin gaskantawa da Kristi ba. Gaskiyar ma ita ce sun gaskanta da shi ne domin Allah ya basu rai na har abada. Sun gaskanta ne domin Allah ya rigaya ya cece su.

| |
|---|
| *Gaskiyar ita ce sun gaskanta da shi ne domin Allah ya basu rai na har abada* |

### *Kristi Yayi Dukan Aikin - Yayi Aminci- Domin Ceton mu*

Yayinda Allah yake rubuta Littafi Mai-Tsarki, bai bari a gane gaskiya da sauri ba. Ya sa mu dole mu ƙasƙantar da kanmu yayinda muke neman hikima daga Allah a cikin ƙoƙarin mu na binciken waɗannan ayoyin masu wuya a hankali. A kowane lokaci ya kamata mu riƙa tunawa da cewa ba zamu sani cewa mun fahimci Littafi Mai-Tsarki ba sai idan mun sami dukan abin da Littafi Mai-Tsarki yake mawafuka da juna.

Wani abu mai wuyar warwarewa da Littafi Mai-Tsarki ya ƙunsa yana samuwa a cikin ayoyin Galatiyawa sura 2 da Galatiyawa sura 3. A misali, Galatiyawa 3:2 na cewa:

**Wannan kaɗai ni ke so in tambaya a gareku, ta wurin ayyukan shari'a kuka karɓi Ruhu (kuka sami ceto), ko kwa ta wurin labari na bangaskiya?**

Ka tuna cewa bangaskiya aiki ne. Amma wanene yayi dukan aikin ceton mu? Yesu ne yayi dukan aikin. Yayi aminci a cikin dukan dokokin Allah ya kuma kawo mana ceto. Domin haka, muna iya fasara Galatiyawa 3:2 kamar haka; "Kun karɓi Ruhu ta wurin aikin kiyaye shari'a ko kuwa ta wurin labari na bangaskiya (aikin da Kristi yayi domin ya cece mu)?" Wannan shi ya sa sunansa ya zama Mai-aminci (Ruya ta Yohanna 19:11). Shine cikakken aikin bangaskiya.

Galatiyawa 2:16 ta ce:

**Amma mun sani mutum ba za shi barata bisa ga ayyukan shari'a ba, sai ta wurin bangaskiya cikin Yesu Kristi, mu da kanmu muka bada gaskiya ga Kristi Yesu, domin mu barata ta wurin**

**bangaskiya cikin Kristi ba bisa ga ayyukan shari'a ba: gama bisa ga ayyukan shari'a, ba mai rai da za shi barata.**

Mutum baya samun barata ta wuirn ayyukan shari'a sai ta wurin bangaskiya, aikin Kristi. Yayi aminci cikin dukan ayyukan da ake bukata domin ceton mu.

Yawancin lokaci zamu fi samun sauƙin fahimtar ayoyin da suka ƙunshi kalmar nan "bangaskiya" idan muka musanyata da kalmar nan "Kristi," wanda sunansa "Mai-aminci." Ta haka, zamu iya fahimtar Afisawa 2:8 kamar haka, "Bisa ga alheri an cece ku ta wurin bangaskiya (Kristi)." Galatiyawa 3:11 kuma haka, "Mai adalci ta wurin bangaskiya (Kristi) za shi rayu." Za mu kuma fahimci Galatiyawa 3:2 haka, "Ta wurin ayyukan sharia'a kuka karɓi Ruhu, ko kwa ta wurin labari na bangaskiya (ko kuma jin labarin Kristi, wato Maganar Allah)?"

### *A Kowane Lokaci, Allah ne ke Aikin Hatimcewa*

Wata karkatattar koyaswar Littafi Mai-Tsarki da malaman Littafi Mai-Tsarki ke yi a cikin ikklisiyoyi shine koyaswar nan da ke cewa baftisma ta ruwa tana hatimce mutum a cikin alkawali ko kuma cikin adalci.

Sun kafa wannan gurguwar koyaswar a bisa Romawa 4:11 inda muka karanta cewa:

**Ya kwa karɓi alama ta kaciya, hatimin adilci na bangaskiya wadda ya ke da ita tun yana cikin rashin kaciya: domin ya zama uban masu bada gaskiya duka, ko cikin rashin kaciya su ke, domin a yi lissafin adilci garesu.**

Aikin hatimcewa wani aiki ne na shari'a da Allah ne kaɗai zai iya yinsa. A misali, Allah ya bayyana ceton ɗaya daga cikin zaɓaɓɓun sa a Afisawa 1:13 inda muka karanta cewa:

**A cikinsa ku kuma, da kuka ji maganar gaskiya, bisharar cetonku - a cikinsa, sa'anda kuka bada gaskiya kuma, aka hatimce ku da Ruhu Mai-Tsarki na alkawali.**

A cikin wannan ayar, Allah yana nuna cewa sun ji maganar Allah (bangaskiya na zuwa a wurin ji), suka fara

gaskantawa da Littafi Mai-Tsarki, sun bada gaskiya (Yunana 3:5), kuma domin su zaɓaɓɓu ne na Allah, Allah kuma ya rigaya ya biya bashin zunubansu, Allah ya hatimce su ta wurin basu Ruhu Mai-Tsarki, wanda shine tabbacin cewa Allah ya cece su. Wannan na nuna mana cewa hatimcewa aiki ne na Allah inda Allah yake ba mutumin sabon ruhu.

Sabili da haka ya kamata mu gane cewa Romawa 4:11 tana koyas da wani abu kamar haka ne:

**Ya kwa karɓi alama** (abin al'ajibi) **ta Kaciya** (kaciya ta ruhu, wadda ita ce ceto (Kubawar Shari'a 30:6), **hatimin** (tabbaci) **adalci na bangaskiya** (Kristi) **wadda yake da ita tun yana cikin rashin kaciya** (kaciya ta jiki)...

Da wannan fahimtar, mun sani wannan koyaswar ta yi daidai da sauran koyaswa ta Littafi Mai-Tsarki game da ceto.

### *Ba kowane lokaci bane yake Zama Dole A yi Gyara a Fassarar*

Muna iya cewa zamu iya yarda da waɗanda suka fassara Littafi Mai-Tsarki daga Ibraniyanci da Helinanci zuwa juyin turanci na King James Version wanda shine juyin turanci mafi inganci. Sai dai kuma su ba horarru bane daga Allah kamar mutane masu tsarkin da Allah yayi amfani da su suka rubuta Littafi Mai-Tsarki na ainihi wanda ya fito daga bakin Allah, sabili da haka, masu juyawar suna iya yin kuskure. Idan kuma muka dubi waɗansu ayoyi waɗanda suka yi magana game da samun ceto, sai mu ga cewa hakika juyin na su yayi daidai. Ka tuna cewa juyin ne yayi daidai amma ba Ibraniyanci ko Helinanci na ainihin ba.

Gaskiyar ita ce, yayinda muke ƙoƙarin haɗa ayoyin Littafi Mai-Tsarki da juna, mun gano cewa akwai babbar matsala a cikin juyin Littafi Mai-Tsarki. Yawancin lokaci, masu juya Littafi Mai-Tsarkin, wannan kuma haka yake musamman ma ga waɗanda suka juya Littafin zuwa turanci na King James Version, sun yi ƙoƙari su tabbatar cewa sun yi aminci wajen juyawa daga juyin Tsohon Alkawali na Ibraniyanci da kuma juyin Sabon Alkawali na Helinanci.

Sai dai kuma akwai waɗansu ayoyi a cikin Littafi Mai-Tsarki da suke da alamar sun yarda da juna idan ka dubi yadda aka juya su, amma a gaskiya, sun haifar da wata babbar matsala musamman ma yadda wannan ya shafi saƙon ceton Allah. Sun ƙunshi ra'ayin yadda bangaskiya take kawo ceto. Ka lura da yadda waɗannan ayoyin suka yarda da juna:

Farawa 15:6: **Ya fa bada gaskiya ga Ubangiji; shi kuwa ya lissafta wannan adilci ne gareshi.**

Romawa 4:3: **Gama me nassi ya ce? Ibrahim kwa ya bada gaskiya ga Allah, aka lissafta wannan adalci gareshi.**

Romawa 4:9:**To wannan albarka, masu kaciya ne kawai ake yi wa, ko kuwa har da marasa kaciya ma? Gama abinda muke cewa shi ne. "Aka lasafta bangaskiyar Ibrahim adalci ce a gare shi."**

Galatiyawa 3:6 **Kamar yadda Ibrahim ya gaskanta Allah, aka kwa lissafta wannan adilci a gareshi**

Waɗannan ayoyin suna koyaswa kai tsaye cewa ceto yakan samu ga wanda ya gaskanta da Yesu a matsayin Mai-ceto, kuma wannan matsayin shine ake koyaswa game da shirin ceto na Allah a kusan kowace ikklisiya.

*A duk lokacin da muka yi biyayya da wata doka ta Littafi Mai-Tsarki har ma da dokar da ke cewa mu bada gaskiya ga Kristi, aiki ne muke yi*

Sai dai wannan matakin bashi yiwuwa. Bangaskiya ga Kristi aiki ne da muke yi. Ka tuna cewa a duk lokacin da muka yi biyayya da wata doka ta Littafi Mai-Tsarki har ma da dokar da ke cewa mu bada gaskiya ga Kristi, aiki ne muke yi. Kuma kamar yadda muka rigaya muka koya, babu wani aikin da zamu yi wanda zai iya taimaka mana ko kuma gabatar da mu wajen samun ceto. Bangaskiya shine a gaskanta, kuma Littafi Mai-Tsarki ya faɗa a fili cewa bangaskiya aiki ne.

Mun karanta a 1 Tassalunikawa 1:3 cewa:

**Ɓa bu fashi, muna tunawa da aikin bangaskiyarku da ɗawainiyar ƙamnarku da hanƙurin begenku cikin Ubangijinmu Yesu Kristi, a gaban Allahnmu Ubanmu.**

Mun kuma karanta a 2 Tassalunikawa 1:11 cewa

**Saboda wannan fa kullum muna addu'a dominku, Allahnmu shi maishe ku, ku cancanci kiranku, ya kuma biya kowane muradin nagarta da kowane aikin bangaskiya, bisa ga ikonsa**

| |
|---|
| *Tsayawa akan matsayin cewa idan ka bada gaskiya da Kristi zaka sami ceto wani abu ne wanda bashi yiwuwa* |

Sabili da haka, Tsayawa akan matsayin cewa idan ka bada gaskiya da Kristi zaka sami ceto wani abu ne wanda bashi yiwuwa. Abin baƙin cikin shine wannan koyaswa mai cewa gaskantawa da Kristi kawai zai taimaka mana wajen samun ceto na shinfiɗa wani shiri na ceto wanda yake daidai da aikin da mutumin na yayi a cikin Lissafi 15, wanda ya tsinci ƙiraren itace a ranar Asabaci, sabili da haka, a bisa umurnin Allah, aka jejjefeshi har ya mutu. Ka tuna da ranar Asabaci, ranar da babu wani aikin da za'a yi, ya zama wani hoto ne na wata koyaswa da ke ƙarfafa cewa kada mu yi tunani ko da ɗan kaɗan cewa wani aikin da zamu yi zai iya taimaka mana wajen samun ceto.

Nan take mun ga irin ɓarnar da ke kafe a cikin kowace ikklisiya. Suna koyas da wani shiri na ceto wanda yake sa dukan mutumin da yake tsammani yana da ceto domin ya gaskanta da Kristi a matsayin nan da mutumin nan da ya tsinci ƙiraren itace a ranar Asabaci ya sami kansa. Har yanzu wannan mutumin yana ƙarƙashin fushin Allah. Wannan wani mugun al'amari ne.

To ta yaya ya kamata a juya waɗannan ayoyin? Za mu dubi kowane ɗayansu da tunanin cewa bangaskiya aiki ne.

### *Ko Ibrahim ya Sami Ceto ne Sakamakon Gaskantawa da Allah?*

Da farko dai zamu duba Farawa 15:6. A cikin juyi na King James, juyin yana kamar haka:

**Ya fa bada gaskiya ga Ubangiji, shi kuma ya lissafta wannan adilci ne a gareshi.**

Da alama wannan ayar tana tabbatas mana cewa bangaskiyar Ibrahim ce aka lissafta adalci a gareshi, wato, Allah ya cece shi domin ya gaskanta.

*Bangaskiya aiki ne da muke yi, kuma aikin mu ba zai taɓa zama sanadiyar ceton mu ba*

Sai dai kuma kamar yadda muka koya, wannan bashi yiwuwa domin gaskantawa aiki ne da muke yi kuma babu wani aikin mu da zai taɓa zama sanadiyar ceton mu. Wurin nan da wannan ayar ke samuwa na nuna mana cewa bangaskiyar Ibrahim, bangaskiya ce ta wanda ya rigaya ya sami ceto. Dole ne mu tuna cewa idan Allah ya cece mu, za mu yi ayyuka nagari, amma ko kaɗan waɗannan ayyukan, har ma da bangaskiya ciki, basu taimaka mana wajen samun ceto. Dukansu sakamako ne na ceton da muka samu.

Mu kuma lura da cewa a cikin Ibraniyanci, akan iya fassara "da" ya zama "sabili da.' Saboda haka, a cikin wannan ayar kalmar nuna dagantaka 'da' ya kamata a fassara ta 'sabili da'.

Matsala ta biyu ita ce fahimar kalmar nan ta wakilin suna "wannan." A ilimin nahawu kalmar nan ta wakilin suna "wannan" daidai sai dai kuma wace Kalmar suna ce take magana a kai? Shin "wannan" na magana ne akan bangaskiyar Ibrahim ne? Wannan bashi yiwuwa domin manyan dalilai guda biyu. Na farko shine ba yanda za'a yi a lissafta bangaskiyar Ibrahim a matsayin adilci.

Babbar matsala ta biyu ita ce a cikin wannan bayani kalmar wakalin suna 'wannan' a ilimin nahawu tana nuna Kalmar mace. Kalmar suna ta 'bangaskiya' kalmace ta namiji. Saboda haka, a ilimin nahawu, kalmar wakin suna ba za'a danganta ta da bangaskiyar Ibrahim ba.

A wani fannin kuwa kalmar 'adalci' ta sunan mace ce kuma tafi dacewa dai dai a cikin wannan ayar. Sabili da haka ya kamata mu fahimci Farawa 15:6 kamar haka:

**Ya** (Ibrahim) **fa bada gaskiya ga Ubangiji** (Allah)**, domin shi** (Allah)**, ya lissafta wannan** (adacin Allah) **adalci ne** (ceton Ibrahim) **a gareshi** (Ibrahim).

Haka kuma, a cikin Romawa 4:3, Galatiyawa 3:6, da kuma Yakub 2:23, juyin King James ya ce "Ibrahim ya gaskanta Allah an kuwa lissafta wannan adalci ne a gareshi" Idan an dube su yadda aka juya su, da alama waɗannan ayoyin suna koyas da cewa bangaskiyar Ibrahim ce ta sa Allah ya cece shi. Amma kamar yadda muke ta faɗi, wannan bashi yiwuwa. Sabili da haka ya kamata mu tabbatas da cewa an juya waɗannan ayoyin daidai.

Akwai kalmomi guda biya a cikin juyin da ya kamata a gyara domin waɗannan ayoyin su yi daidai da koyaswar Littafi Mai-Tsarki cewa Allah ne yayi dukan aikin ceto. Har yanzu dai kalma ta farko da ke bukatar canji ita ce dangantawa "kuma" ya kamata a juya ta ta zama "domin." Kamar yadda yake a cikin harshen Ibraniyanci, haka kuma a cikin harshen Helinanci za'a iya juya kalmar nan "kuma ko kuma a wani lokaci akan fassarata a matsayin kalmar 'domin'.

Kalma ta biyu da take bukatar a canza ta ita ce "wannan." A yadda yake, ya kamata da an juya kalmar "wannan" a ilimin nahawu wannan kalma ce makaɗaiciya mai nuna mutum na ukku "shi." Ta haka za a jadada Romawa 4:3, Galatiyawa 3:6 da Yakub 2:23, ya kamata juyin ya fita kamar haka, "Ibrahim ya gaskanta Allah (ya sami ceto), domin an lissafta masa (Ibrahim) shi (Allah) adalci (ceton Ibrahim)."

### *Kristi na iya Ceton mu Idan muka Gaskanta da Shi*

Yanzu da yake mun koyi cewa Yesu Mai-Ceto ne yayi dukan aikin ceto kuma bai kamata ko kaɗan mu gaskanta cewa akwai wani aiki da zamu iya yi da zai taimaka wajen ceton mu ba, yanzu zamu fi ganewa da waɗansu ayoyin da suke koyar da abin da ya saɓawa haka.

A misali, a cikin Galatiyawa 2:16, Allah ya furta cewa:

**Amma mun sani mutum ba shi barata bisa ga ayyukan shari'a ba, sai ta wurin bangaskiya cikin Yesu Kristi, mu da kanmu muka bada gaskiya ga Kristi Yesu, domin mu barata ta wurin**

**bangaskiya cikin Kristi, ba bisa ga ayyukan shari'a ba: gama bisa ga ayyukan sharia ba mai rai da za shi barata**

Kashi na farko na wannan ayar a bayyane yake. Ba yin biyayya da wata dokar Littafi Mai-Tsarki (ko kiyayye dokoki) ke ceton mu ba, amma ta wurin bangaskiya (aikin gaskantawa), cewa Yesu yayi aikin domin ceton zaɓaɓɓu.

Amma kashi na biyu na ayar yana iya rikitaswa. Idan ka duba, kamar wannan sashen yana koyas da cewa idan muka gaskanta da Kristi, Kristi zai baratas (cece) da mu. Ko da yake Allah ya sake faɗar cewa "Ta wurin ayyukan shari'a, ba mai rai da zashi barata," duk da haka wannan wurin yana iya ɓad da mutum. Ka tuna kuma gaskantawa aiki ne na shari'a.

Tunda gaskantawa aiki ne na shari'a, ta yaya zamu fahimci "Mu da kanmu muka bada gaskiya ga Kristi Yesu domin mu barata"? A bisa haruffan Helinanci, kalmomin "domin mu barata" ba kalmomi ne masu ƙarfi ba. Kamar yadda yake a cikin turanci, za'a iya yin amfani da irin waɗannan kalmomin ta hanyar da zai nuna cewa abu yana iya faruwa sai dai ba lalle ya faru ɗin ba. An yi amfani da kalmomi masu irin wannan manufar da yawa a cikin Littafi Mai-Tsarkin da aka rubuta a cikin harshen Helinanci.

Sai dai kuma a harshen Helinanci, har yanzu akan iya yin amfani da su domin su nuna wata niyya ko kuma wani umurni. A misali, sau da yawa akan yi amfani da irin wannan a cikin Sabon Alkawali domin a nuna cikar wani anabcin dake cikin Tsohon Alkawali. Shi yasa muke karanta abubuwa kamar su "Domin a cika" (Matta 4:14, 8:17, 12:17). Waɗannan kalmomin "domin a cika" kalmomi ne da ke iya faruwa sai dai ba lalle su faru ba. A wannan wurin babu wata shakka game da waɗannan kalmomin. Anabcin ya cika.

Idan muka koma Galatiyawa 2:16, mun sani cewa tun da bangaskiya wani aiki ne da muke yi, bangaskiyarmu ba zata taba tabbatas mana da ceto ba. Bangaskiyarmu na iya samu mu yi ƙoƙarin yin biyayya da umurnin Littafi Mai-Tsarki na samun ceto, yin addu'a, tuba da dai sauransu, amma mun sani ceton mu yana hannun Allah ne, ya danganta ga ko muna cikin zaɓaɓɓu na Allah, ko ya biya bashin zunuban mu ko babu.

*Ceton mu yana hannun Allah ne, ya danganta ga ko muna cikin zaɓaɓɓu na Allah, kuma ya biya bashin zunuban mu.*

Sabili da haka dole ne mu fahimci kalmomin nan "don mu barata" da ma'anar barata (ceto) na iya yiwuwa, sai dai mutum ba zai tabbatas cewa wai don yayi aikin bangaskiya zuwa gareshi ba. Mutane Nineva a cikin Yunana sura 3 sun gaskanta da cewar Allah zai hallakar da su a cikin kwanaki 40. Sabili da haka sun yi biyayya da maganar Allah cewa su tuba (Yunana 3:8-10). Sai dai kuma sun gane sarai cewa ba su sani ba ko Allah zai jiƙan su ko babu. Kila, Allah ya cece su. Yana yiwuwa a cece su daga hallaka. Ta haka, Galatiyawa 2:16 na koyas mana cewa idan mu mutanen da bamu da ceto muka gaskanta shari'ar Allah, Allah yana iya ceton waɗansun mu.

Ka tuna da wannan gaskiyar cewa babu wanda zai iya sanin ko yana cikin zaɓaɓɓu na Allah ko babu sai bayan da ya sami ceto, an nanata wannan a Joel 2:13-14:

**Ku tsaga zukatanku ba tufafinku ba, ku juyo wurin Ubangiji Allahnku: gama shi mai alheri ne, cike da juyayi, mai jinkirin fushi, mai yalwar jinƙai, yana sake nufinsa a kan masifan da ya shirya. Wa ya sani ko ba za ya juya ya sake nufinsa ba, ya bar albarka a bayansa, watau hadaya ta gari da ta sha ga Ubangiji Allahnku?**

Haka kuma an nanata wannan a cikin Zephaniah 2:3:

**Ku biɗi Ubangiji, ku dukan masu tawali'u na duniya, ku waɗanda kuka kiyaye shari'arsa, watakila a boye ku a cikin ranar fushin Ubangiji**

Haka kuma a ayoyi kamar su 2 Korantiyawa 2:4 da 2 Korantiyawa 11:7, Allah yayi amfani da irin waɗannan kalmomin waɗanda suka yi kama da kalmomin nan "domin mu barata" wanɗanda ke cikin Galatiyawa 2:16. A cikin 2 Korantiyawa 2:4 an juya kalmomin zuwa "domin a baƙanta muku ciki ko rai," a cikin 2 Korantiyawa 11:7 kuma an juya shi zuwa "domin ku ɗaukaka" cikin dukan ayoyin nan biyu, an yi amfani da kalmomin

domin su nuna wani abu da ke iya faruwa ba wai wani abu da ya zama tabbatacce ba.

*Ruɗani a cikin Fahimtar Kalmar nan "Gaskantawa"*

Wani babban darasi da muke koyo shine, Allah bai bar fahimtar shirin sa na ceto a sauƙaƙe ba. Allah ya sanya kalmomin nan "gaskantawa" da "bangaskiya" a cikin ayoyi da yawa, kuma sai ta wurin yin amfani da sharaɗin da Allah ya kafa na kwatanta aya da aya da kuma ta wurin neman hikima daga Allah ne kaɗai zamu iya harhaɗa waɗannan ayoyin.

| |
|---|
| *Allah bai bar fahimtar shirinsa na ceto ya zama da sauƙi ba* |

Waɗansu abubuwa game da gaskantawa da suka fito sun haɗa da:

1. Dole ne a fahimci kalmomin nan "gaskantawa" da "bangaskiya" a matsayin aiki da ake yi. Wannan ya zama haka kuwa domin Yesu ya gama dukan aikin da ake bukata domin ceton zaɓaɓɓu domin kuma sunansa "Mai-aminci" (Ruya ta Yohanna 19:11). Shi ne asalin aikin bangaskiya.

2. Idan mutum ya bada gaskiya, ko da a wanne mataki, bangaskiyarsa aiki ne wanda yake yi wanda ba zai taɓa iya zama cikin abin da ake bukata domin ceton sa ba. Idan ya gaskanta, kila yana yin haka ne domin lamirinsa ya sa shi ya gaskanta ko kuma kila Allah ne yake aiki a cikinsa. Sai dai kuma ba zai taɓa sanin ko wanne dalili ba ne sai dai idan ya zo daga baya ya sami ceto, zuciyarsa cike take da mugunta domin haka ba zai iya gaskantawa da dukan zuciyarsa ba.

3. Idan mutum ya gaskanta bayan ya sami ceto, wannan ma aiki ne wanda yake yi. Sai dai kuma, gaskantawar shi zata zama da dukan zuciyarsa domin a wannan lokacin Allah ya rigaya ya cece shi, ya kuma bashi sabuwar zuciya. Gaskantawa da dukan zuciyarsa (bayan ya sami ceto) na nufin cewa ceton sa zai zama cikakke a ƙarshen duniya lokacin da za'a bashi rayayyen jiki na ruhaniya wanda zai kasance har abada. Wannan

zai faru ne domin aikin da Kristi yayi na ceton mu ya shafi dukan fannin rayuwarmu. Sabili da haka, Littafi Mai-Tsarki yayi amfani da kalmomin nan "gaskantawa" da "bangaskiya" a matsayin aikin da mutum ke yi wanda bai kamata a danganta shi da wata hanya ko kuma wani abin da yake kawo ceto ba.

4. Dukan wani shiri na ceto wanda bai yi la'akari da waɗannan sharuɗɗan ba, zai ƙarasa da sa mutumin da yake ƙoƙarin bin wannan shirin a matsayin mutumin nan da yake tsintar ƙiraren itace a ranar Asabaci (Lissafi 15). Za'a hallaka shi. Iyakar hanyar gujewa wannan mugun ƙarshen rayuwar shine a juya wa wannan shirin ceton da mutum ya ƙirƙiro baya, a jira Allah ya ƙarasa dukan aikin ceton mutumin, idan dai har Allah yana da niyyar ceton mutumin.

### *Shaiɗan Ya zo kamar Mala'ikan Haske*

Yanzu da yake mun koya daga Littafi Mai-Tsarki irin munin da dogara ga wani shiri na ceto wanda yayi dabam da abin da Littafi Mai-Tsarki ya bayar, ya kamata mu yi hankali da irin mutanen dake yi mana koyaswa. Wannan yana ɗaya daga cikin wuraren da Shaiɗan ke iya zuwa kamar mala'ikan haske mutanensa kuma kamar masu koyaswar adalci (2 Korantiyawa 11:13-15).

Akwai masu wa'azi da masu bishara da yawa da ake girmamawa sabili da amincin su ga koyaswar Littafi Mai-Tsarki. Ana ɗaukaka su ƙwarai. Ana darajantasu a matsayin bayin Allah. Suna koyas da cewa Littafi Mai-Tsarki maganar Allah ce marar aibi. Suna wa'azinsu kai tsaye daga Littafi Mai-Tsarki. Amma game da muhimmancin ceto da kuma albarka da ke tare da samun ceto sukan ce, "Kai ma zaka iya samun ceto yau. Ka bada gaskiya ga Yesu a matsayin Ɗan Allah ka kuma karɓe shi ya zama Mai-cetonka." Sukan faɗi waɗannan a matsayin ƙarfafawa a cikin hanyar ƙauna da kuma kulawa. Akwai alamu da yawa na cewa su bayin Allah na gaskiya ne. Ba a cikin sunan Allah suke wa'azi daga cikin Littafi Mai-Tsarki ba?

| |
|---|
| *An ruɗe su har suna bin wani shiri na ceto wanda tabbas zai kai su ga hallaka* |

Kuma dukan hanyoyin samun ceton da suke bayaswa suna da kyau a ido domin mutane suna tunanin cewa, "Nima, yanzu yanzu, zan sani cewa an gafarta mani zunubaina, kuma zan kasance a cikin Kristi har abada." Sabili da haka waɗanda suka yarda da waɗannan masu koyaswar suka kuma bi abin da suke cewa sun yarda cewa sun kafu a cikin Kristi har abada. An ruɗe su har suna bin wani shiri na ceto wanda tabbas zai kai su ga hallaka. An ruɗe su zuwa gaskantawa da bisharar ƙarya. Abin baƙin cikin shine suna kama da mutumin nan wanda yake tsintar ƙiraren itace a ranar Asabaci

A cikin 2 Korantiyawa 11:14, Allah yayi kashedin cewa Shaiɗan yakan zo kamar mala'ikan (manzon) haske. Kristi shine Manzon haske na gaskiya. Amma ta wurin ma'aikatansa na adalci, Shaiɗan yakan zo da kamannin Kristi. Waɗannan ma'aikatan jabun Kristi ne. Sun gaskanta cewa suna bautawa Kristi ne amma a gaskiya, ubangijinsu Shaiɗan ne, maƙiyin Kristi.

Irin koyaswar su wadda ba ta yi dabam da koyaswar sauran malaman Littafi Mai-Tsarkin da ake ji da su ba tana samuwa a ko'ina. Sai dai a cikin dukan koyaswar, akwai babbar kaucewa gaskiyar cewa Kristi ya gama dukan aikin da ake bukata domin ceton mutane, kuma ya gama wannan da daɗewa kafin haifuwar mutumin, Kristi ya biya bashin dukan zunuban mutumin. Abin da Littafi Mai-Tsarki yake koyaswa kenan, kuma dole ne mu zama masu sauraron dukan Littafi Mai-Tsarki, mu kuma gane cewa Kristi ne ya kamata ya karɓi dukan ɗaukaka domin ceton mu amma bamu da kanmu ba.

Waɗannan masu wa'azin da masu shelar bishara suna ganin kansu a matsayin masu ƙwarewa, bayin Kristi na gaskiya, amma gaskiyar ita ce, su "Mai'aikatan adalci" ne na Ibilis (2 Korantiyawa 11:15). Suna zuwa a cikin sunan Yesu Kristi, amma su bayin Shaiɗan waɗanda ke zuwa kamar mala'ikun haske ne (2 Korantiyawa 11:14). Suna shinfiɗa ƙarya a cikin shirin ceton su na jeka-na-yi-ka domin ubangidansu Shaiɗan shine uban ƙareraki (Yohanna 8:44). Abin kaico. Ka yi tunanin mutanen dake sauraron suna kuma gaskantawa da su, yayinda suke ƙarɓar wannan ƙaryar, suna ɗaure kansu a hanyar da ba ta da bege.

Sabili da haka, wannan yana da muhimmanci ƙwarai. Kila kayi shekaru kana gaskanta cewa kana da ceto domin an koya

maka cewa idan ka "karɓi" Yesu a matsayin Mai cetonka, to ka tsira. Kila har ka zama mai bada shawara a ikklisiyarku, sabili da haka, kayi shekaru kana tunanin cewa ka tsira, kana hannun Yesu.

Yanzu kuma ka ruɗe, ka gane cewa kana nan a matsayin mutumin nan mai tara ƙiraren itace a ranar Asabaci. Har yanzu kana ƙarƙashin hukumcin Allah, kana jiran lokacin hallakar ka. Idan dama kai malamin Littafi Mai-Tsarki ne ka kuma koyas da mutane da yawa ka sa su a tarkon shirin ceto na jeka-na-yi-ka, kana jagorantarsu zuwa hallaka, naka ya fi muni.

Sabili da haka lalle wannan tambaya "Shin ko akwai bege domina? Ko nima Allah zai iya gafarta zunubaina?" ba zata bar ka ba.

Amsar da ke fitowa daga Littafi Mai-Tsarki ita ce, Kristi yazo domin masu zunubi. kamar kowa, kai ma kana da begen samun ceto. Kai ma kana bukata ka tuba daga zunubin bin bishara ta ƙarya, ka yi addu'a, ka kuma yi begen kila Allah a cikin girman jinƙansa ya zaɓe ka domin ya cece ka.

Abin mamaki shine, wannan shirin ceto na jeka-na-yi-kan yana nan a cikin kusan kowace ikklisiya. Ta yaya abin ya zama haka? Matsalar ita ce waɗannan ikklisiyoyin basu yin amfani da dukan Littafi Mai-Tsarki, kuma basu bin koyaswar Littafi Mai-Tsarki a hankali suna kwatanta nassi da nassi. Haka kuma, basu gane cewa ko da yake an rubuta Littafi Mai-Tsarki da harshen mutane, ba zamu iya fahimtar babban saƙon da ya ƙunsa ba sai idan mun sami koyaswa ta ruhaniya a cikin waɗannan kalaman dake rubuce a harshen mutane. Wato, suna da karkatattar koyaswa, karkatacciyar hanyar fasara Littafi Mai-Tsarki (Markus 4:33-34). Sai dai kuma, akwai wani babban dalilin da ya sa waɗannan karkatattun bisharun da karkatattun shirye shiryen ceto suke da yawa a cikin ikklisiyoyi.

### *Ko Akwai Yadda Za a Iya Kiyaye Tsarkin Ikklisiya?*

Kowace ɗarika ta faɗa cikin tarko, abin da ya faru kenan. Kila a cikin marmarinsu na kiyaye ikklisiya da tsarki, Shugabannin addinai sun yi ƙoƙari su bar cetattu kaɗai a cikin ikklisiyoyinsu. Domin su iya cimma wannan, kowacce ikklisiya ko ɗarika ta fito da wani tsari, wata hanya, ko wani shiri da suke yin amfani da shi. Kila iyakar abin da suke bukata mambobinsu

su yi shine su yi shaidar bangaskiya, ko su furta cewa sun gaskanta da Kristi a matsayin Mai cetonsu. Amma yawancin lokacin abin da yake faruwa shine, shugabannin ikklisiyoyin suna neman a yi wa mutum baftisma cikin ruwa ya kuma yi alkawalin cewa a matsayinsa na memban wannan ɗarikar, zai yi biyayya da dukan koyaswar wannan ikklisiyar.

*A maimakon haka, abin nan da suka kafa ko kuma wannan tsarin da suka yi domin tabbatar da ceto, ya haifar da wani abu dabam*

Abin baƙin cikin shine abin nan da suka kafa ko kuma shirin da ikklisiyoyin suka tsara bai bi sharuɗɗan Littafi Mai-Tsarki ba, wato, idan muka yi biyayya da wata doka ta Allah muka kuma gaskanta cewa yin biyayya zai taimaka mana wajen samun ceto, muna kama da mutumin da yake tsintar ƙiraren itace a ranar Asabaci (Lissafi 15). Har yanzu muna ƙarƙashin fushin Allah. Ta haka, abin nan da suka kafa ko kuma wannan tsarin da suka yi domin tabbatar da ceto, ya haifar da wani abu dabam. Ya taimaka wajen riƙe mutane a cikin yanayinsu na marasa ceto.

Wannan mummunan yanayin shine ya sa a cikin kwanakin nan na mu, mafiya yawa a cikin ikklisiyoyin mu ba su sauraron kashedin nan cewa Shaiɗan shine ke mulki a cikin ikklisiyoyi a yau, ba su sauraron kashedin nan na cewa su fito daga cikin ikklisiyoyi domin kada su shiga bautar Shaiɗan a cikin ikklisiyoyin. Kuma suna watsi da wannan babban kashedin na cewa ƙarshen duniya ya kusa. (Idan kana son ƙarin bayyani a kan waɗannan, ka tuntuɓi Family Radio ka nemi a aika maka da waɗannan littattafan kyauta: Mun Kusa Ga Karshe, Ɗaukaka Ga Allah, Lokaci Na Da Iyaka, Abin Da Ya Biyo Bayan Karshen Zamanin Ikklisiya, da kuma Alkama da Zawan.)

Duk da shirin ceton da ya saɓawa Littafi Mai-Tsarki wanda ya bazu ko'ina cikin ikklisiya, an sami 'yan mutane ƙalilan a cikin zamanin ikklisiya waɗanda suka sami ceto. Kila suna da ɗan sani ko kuma cikakken sanin abin da wannan ikklisiyar ke koyaswa, amma Allah ya cece su domin an zaɓe su domin ceto. Suna ƙarƙashin sauraron Littafi Mai-Tsarki, Allah kuma ya cece su. Sabili da haka, sun sami wani marmarin yin biyayya da

koyaswar Littafi Mai-Tsarki.  Wannan kuwa ya faru koda yake kila iliminsu na  Littafi Mai-Tsarkin su ƙalilan ne.

*Ya kamata mu koyar da cewa ya kamata mutumin da bashi da ceto yayi ƙoƙari ya yi biyayya da dokokin Allah, yana kuma addu'a, domin idan Allah ya yarda, ya saka shi a cikin shirinsa na ceto.*

Ikklisiyoyi sun kasa fahimtar cewa babu wani shiri na mutum, komi binshi da kyau da aka yi, da zai tabbataswa mutum da ceto, kuma ya kamata faɗuwarsu ta zama babban darasi a garemu.  Yayinda muke aikawa da Bishara a cikin duniya, bai kamata mu bayar da wani shiri ko wani tsari na mutum har mu kai ga cewa idan an bi wannan shirin ko tsarin da kyau, zai tabbatar wa mutum da ceto ba.  Ya kamata mu koyar da cewa ya kamata mutumin da bashi da ceto yayi ƙoƙari ya yi biyayya da dokokin Allah yayinda yake bege, yana kuma addu'a, domin idan Allah ya yarda, ya saka shi a cikin shirinsa na ceto.

### *Babbar Sake Kama*

Yanzu dole ne ayi tambayar nan: Ta yaya ceto yake shafar rayuwar mutum?  Kuma menene ake nufi da maya haihuwa?

Ka tuna cewa kafin mutum ya sami ceto, yana kama da kowane mutumin da ba zaɓaɓɓe ba  a cikin hali da kuma tabi'a. Yana marmarin zunubi da kuma yiwa Allah tawaye a cikin jiki da kuma ruhu.

Amma yanzu sai ya sami ceto, an bashi sabon rayayyen ruhu.  ya zama sabon halitta a cikin Kristi.  Lokacin da aka haife shi haihuwa ta jiki, yanayinsa ya ƙunshi jiki da kuma ruhu.  A lokacin ceto, ana maya haihuwarsa, wato, an bashi sabon ruhu. Wannan wata mu'ujjiza ce da hankalinmu na mutumtaka ba zai iya fahimta ba, kuma babu wata alamar rikiɗa ta waje.

Sai dai kuma, za a iya ganin sakamakon canzawar sa ta ruhu, wato, sabon ruhu a cikin tsohon jikin mutumin zai shafi halayyar mutumin har ya kai ga canza rayuwarsa.

Furcin Allah ya tabbatar da wannan domin a cikin 1 Yohanna 3:9 ya ce:

**Dukan wanda shike haifaffe daga wurin Allah bai aika zunubi ba, gama irinsa yana cikinsa zaune: kuma ba shi iya aika zunubi ba, domin an haife shi daga wurin Allah.**

*Allah ya koya mana cewa wani babban canji yakan faru a cikin yanayin mutum a daidai lokacin da mutumin yake samun ceto*

A cikin wannan ayar, Allah ya koya mana cewa wani babban canji yakan faru a cikin yanayin mutum a daidai lokacin da mutumin yake samun ceto. Ba ya iya aikata zunubi a cikin sabon rayayyen ruhunsa. Tun da zunubi ƙetare shari'ar Allah ne, wannan na nufin cewa ba zai iya ƙirƙiro zunubi a cikin sashen sabon ruhunsa ba. Wannan na nufin cewa yana ƙaunar Allah da dokokin Allah a cikin ruhunsa. Wannan na nufin yana da babban marmarin yin biyayya da dukan dokokin Allah dake rubuce a cikin Littafi Mai-Tsarki. Wannan na nufin cewa a cikin sabon ruhunsa, yana raye cikin ruhaniya.

Tun da Allah ya gama dukan abin da ake bukata domin samun ceto (ya zaɓe shi, ya biya fansar zunubansa, ya kuma bashi sabon rayayyen ruhu, abubuwa da duka ake bukata domin ceton dukan zaɓaɓɓu), wannan mutumin zai iya tabbatar da cewa ba zai taɓa rasa cetonsa ba. Irin da yake a cikinsa shine Kristi (Galatiyawa 3:16). Da zaran ya sami ceto, to yana da tabbaci na har abada. Allah ya rigaya ya gama dukan abin da suka zama dole domin ya bashi rai na har abada. Sabili da haka, mai bi na gaskiya ba zai taɓa rasa cetonsa ba. Littafi Mai-Tsarki ya ce babu wani zunubi, ko wani abu da zai iya raba mai bi na gaskiya da ƙaunar Allah (Romawa 8:35-39).

## Mutumin da Ya Sami Ceto Yana Zaune Gangar Jikin Da Ba shi Da Ceto

A cikin sabon ruhunsa, har yanzu mai bi yana zaune a cikin tsohon jikinsa da bai sake ba ko kaɗan lokacin da ya sami ceto. Saboda haka, ya zama mutum mai sha'awa iri dabam dabam guda biyu. A wani ɓangaren kowanne lokaci yana so ya yi biyayya da dokokin Allah, a wani ɓangaren kuma, har yanzu yana sha'awar zunubi. Allah ya bayyana wannan matsayin marar

daɗi yayinda Manzo Bulus ƙarƙashin ikon Ruhu Mai-Tsarki ya faɗa a Romawa 7:21-24 cewa:

**Na iske wannan ka'ida fa a wurina, ni da ni ke nufin in aika nagarta, ga mugunta gareni. Gama ina murna da shari'ar Allah bisa ga mutun na ciki: amma ina ganin wata shari'a dabam a cikin gaɓaɓuwa na, tana yaƙi da shari'ar hankalina, tana saka ni bauta ƙalƙashin shari'ar zunubin nan da ke cikin gaɓaɓuwa na. Kaitona, ga ni mutum abin tausai! Wanene za ya tsamo ni daga cikin jikin nan na mutuwa?**

Samun yanci daga jikin nan mai zunubi wani abu ne da kowane mai bi na gaskiya yake marmarinsa. Sai dai kuma kokowar dake cikin rayuwar da aka ceta ba ƙarama bace. Mutumin da yake da sabon rayayyen ruhu zai iya samun ci gaba da samun nasarar a cikin rayuwar sa (2 Bitrus 3:18). Wannan na yiwuwa ne domin bayan an bashi sabon rayayyen ruhu a lokacin da ya sami ceto, wato, Allah Ruhu Mai-Tsarki ya fara rayuwa a cikin mutumin. A cikin Romawa 8:9 mun karanta cewa idan bamu da ruhun Allah, "mu ba nasa bane."

Bamu fahimci yadda Allah Maɗaukaki zai zauna a cikin rayuwar mutumin da ya sami ceto ba. Dole ne mu yarda cewa wannan wani abu ne da ya wuce ganewarmu. Amma domin mun yarda da Littafi Mai-Tsarki, mun sani cewa haka abin yake, abu ne mai wuyar ganewa sai dai kuma abu ne wanda yake gaskiya. Kasancewar Allah da kansa a cikin rayuwar mutumin da yake da ceto yana ƙara zuga shi wajen yin biyayya da Allah kuma yana marmarin abin da Allah ke so ne kaɗai.

| |
|---|
| *An kuɓutar da cetaccen daga mulkin Shaiɗan, yanzu ya zama na mulkin Kristi har abada.* |

Har wa yau, an kuɓutar da cetaccen daga mulkin Shaiɗan, yanzu ya zama na mulkin Kristi har abada. A cikin Kolossiyawa 1:12-13, Allah ya faɗa mana wannan inda ya ce:

**Kuna bada godiya ga Uban, wanda ya isadda mu mu zama masu tarayya na gadon tsarkaka cikin harke. Wanda ya tsame mu**

**daga cikin ikon dufu, ya maishe mu zuwa cikin mulkin Ɗa na ƙamnarsa**

A cikin Filibiyawa 3:20, mun karnata cewa "yangarancin" mu, wanda za'a iya juyawa "ƙasarmu" na sama. Wannan gaskiya ne ga dukan wanda ya sami ceto.

**Marmarin Mutumin da ya Sami Ceto**

A lokacin da ya sami ceto, abubuwa da yawa waɗanda suke shafar ɗaukar matakai da zasu canza rayuwar da marmarinsa sukan faru a rayuwar mai bi. Zai iya fahimta ya kuma ga yadda kalaman nan da suke samuwa a cikin Zabura 119 da kuma sauran wurare a Littafi Mai-Tsarki. Waɗannan ayoyin suna kaɗan daga cikin abubuwa masu ban sha'awa da ake samu a Zabura 119 waɗanda ke nuna ƙauna da muhimmancin da mai bi na gaskiya yake da shi ga Littafi Mai-Tsarki.

Aya ta 10: **Da dukan zuciya ta na biɗe ka; Kada ka bar ni in ratse dokokinka.**

Aya ta 11: **Na ɓoye maganarka a cikin zuciyata domin kada in yi maka zunubi**

Aya ta 16: **Zan yi daula cikin farillanka. Ba ni mantawa da maganarka**

Aya ta 24: **Shaidunka kuma su ne annishu'wata, su ne kuma abokan shawara ta**

Aya ta 47: **Zan yi daula kuma da dokokinka waɗanda na ƙamnace su**

Aya ta 77: **Bari jiyejiyanƙanka su kawo gareni domin in rayu: gama shari'arka ita ce daulata.**

Aya ta 97: **Ina ƙamnar shari'arka ba misali! Abin tunawa ne a gareni dukan yini.**

Za a iya samun irin waɗannan kalaman ko'ina a cikin Littafi Mai-Tsarki. Duk wanda ya sami ceto da gaske, zai yi ta samun irin wannan marmarin da karfafawar a cikin rayuwarsa. Da haka zai iya gane ya kuma amince da gaskiyar da ke rubuce a 1 Yohanna 2:3-5 inda muka karanta cewa:

**Ta wurin wannan mun sani mun san shi, idan muna kiyaye dokokinsa. Wanda ya ce, na san shi, amma ba ya kiyaye dokokinsa ba, maƙaryaci ne: gaskiya kwa ba ta cikinsa ba: amma wanda yana kiyaye maganatasa, a cikinsa lallai ƙamnar Allah ta cika. Domin wannan mun sani muna cikinsa.**

Mai bi na gaskiya ya sani cewa dokokin Allah sun ƙunshi dukan Littafi Mai-Tsarki. Ya kuma san irin rashin jin daɗin dake faɗo masa idan ya bar sha'awar jiki ta kai shi ga aikata zunubi. Ya nanata wannan da labarin mutumin Allahn nan Dauda wanda ya faɗa a cikin mugun zunubi. Bisa ga jagorancin Ruhu Mai-Tsarki, Dauda ya rubuta babban baƙin cikinsa wanda muke karantawa a cikin Zabura 51.

*Tsoro da Rawar jiki*

Wani hali na mutumin da ya sami ceto na gaskiya shine yana ganin tsarki da adalcin Allah, yana kuma fahimtar cewa Allah shine alkali mai adalci na dukan duniya. A cikin Fillibiyawa 2:12 Allah ya ce:

**... Ku yi aikin ceton ku da tsoro da rawar jiki**

Ceton da mai bi zai yi aikinsa a cikin rayuwarsa shine ceton da Allah ya bashi. Amma yayinda yake girma a cikin alheri (2 Bitrus 3:18), wato, yayinda yake girma cikin ɗaukakar Allah da kuma nisantar sha'awoyin jikin nan mara ceto, yana yin waɗannan da tsoro da rawar jiki.

| |
|---|
| *Da alamar tsayawa gaban Allah da tsoro da rawar jiki bai tafi daidai da tabbacin ceton da wanda yake da ceto ya rigaya ya samu ba* |

Wannan abin mamaki ne domin muna sa zuciyar sakamakon ceton mu zai kawar da dukan tsoron Allah. Da alamar tsayawa gaban Allah da tsoro da rawar jiki bai tafi daidai da tabbacin ceton da wanda yake da ceto ya rigaya ya samu ba. A misali, ya sani cewa Kristi ya rigaya ya biya bashin zunubansa, ya kuma sani cewa maganar hallaka ba zata bashi tsoro ba.

Sai dai kuma dole ne mu tuna cewa Ruhu Mai-Tsarki yana cikin mutumin da ya sami ceto. Kuma mai bi na gaskiya yana girma cikin ƙauna da kuma biyayya da dukan abin da Littafi Mai-Tsarki ke koyaswa. Sabili da haka yana koya yana kuma ƙara yin la'akari da girman Allah. Ya sani cewa Allah shine Mai-iko duka wanda ta wurin maganarsa, dukan duniya ta kasance. Ya sani cewa Allah shine Babban alkali wanda yake sane da dukan zunubanmu kome ƙanƙantarsu. Ya sani cewa Allah Mai-adalci ne sabili da haka kowane zunubi ya cancanci kasancewa a ƙarƙashin fushin Allah. Mai bi na gaskiya ya sani cewa koda yake yanzu da ya sami ceto, biyayyar sa da maganar Allah tana ƙaruwa, amma duk da haka har yanzu yana da wasu zunubai. Yana sane da cewa ba domin jinƙan Allah ba, da shi ma ya cancanci hallaka.

A wani gefen kuma, domin zafin ƙauna da amincewa da Littafi Mai-Tsarkin da mai bi na gaskiya yake da shi, ya sani cewa kasancewarsa a cikin Kristi tabbatacciya ce, ya kuma sani cewa ba zai taɓa ɗanɗana hallaka ba. Ya sani cewa Kristi ya rufe dukan zunubansa. Sai dai kuma, yana ƙara girma cikin sanin Littafi Mai-Tsarki, yana ƙara sanin cewa sakamakon zunubansa, ya cancanci mugun fushin nan na Allah. Ya sani cewa jinƙan Allah da alherinsa ne kaɗai ya bashi ceto. Sabili da haka yana rawar jiki domin tsoro da ganin girman Allah. Ya gane cewa bai cancanci samun ceto ba.

Shi ya sa Littafi Mai-Tsarki yake furta cewa mutumin da ya sami ceto na gaskiya yana tsoron Allah, wannan kuwa shine abin da muka karanta a cikin ayoyi kamar su

Zabura 34:9 **Ku ji tsoron Ubangiji ku tsarkakansa, gama babu rashi ga masu tsoronsa**

Zabura 112:1: **Hallelujah. Mai albarka ne mutum wanda yake tsoron Ubangiji. Wanda yake faranta ransa cikin dokokinsa ƙwarai.**

Misalai 3:7: **Kada ka ga kanka mai hikima ne, ka ji tsoron Ubangiji ka rabu da mugunta kuma.**

Wannan ya nuna gaskiyar cewa waɗanda basu jin maganar Allah, ba su tsoron Allah. Littafi Mai-Tsarki ya nuna wannan a cikin waɗannan ayoyin

Irmiya 44:9-10: **Ko kun manta da muguntar ubanninku, da muguntar sarakunan Yahuda da cikin karabkun Urushalima? Ba su ƙasƙantu ba har wa yau, ba su kwa ji tsoro ba, ba su yi tafiya a cikin shari'ata ko farillai na da na sanya a gabanku da gaban ubanninku ba.**

Irmiya 5:24-25: **Ba su kwa cewa cikin zuciyarsu bari dai mu ji tsoron Ubangiji Allahnmu shi da ke bada ruwa na fari da na baya a lotonsa. shi da ke tanada mana lokacin kaka tabbatacce ne. Muguntarku sun juyadda waɗannan abu, zunubanku sun hana maku alheri.**

Ishaya 57:11-12: **Ina wanda ki ke jin tsoronsa da razana har da kin yi ƙarya ba ki kwa tuna da ni ba, ba ki kwa ajiye wannan a cikin zuciyar ki ba. Ko ban daɗe ina shiru ba har ba ki tsorona ba, zan bayyana a adalcinki: don ayyukan ki kwa ba zasu amfane ki ba.**

Mai'azai 8:13: **Amma babu lafiya ga miyagu, ba kwa za su tsawanta kwanakinsu ba, suna kama da inuwa domin ba su ji ƙwarjinin Allah ba.**

*Cikakkar Kauna tana Kawar da Tsoro*

Gaskiya ne Littafi Mai-Tsarki ya koyas da cewa cikakkar ƙauna ta kan kawas da tsoro. Mun karanta a 1 Yohanna 4:18 cewa

**Babu tsoro wurin ƙauna: amma cikakkiyar ƙauna tana fitarda tsoro, gama tsoro yana da ban wuya wanda yana jin tsoro kwa ba ya kamalta wajen ƙauna ba.**

Zamu iya cewa tunda mai bi na gaskiya ya ɗanɗana cikakkar ƙaunar Kristi, bai kamata ya ji tsoro ba. Wannan gaskiya ne in an bi ta wata hanyar, zamu iya ɗaukar wannan "tsoron" da ake magana akai a wannan ayar ya zama tsoron hallaka ta har abada. Cikakkar ƙaunar Allah zuwa ga mai bi na gaskiya ta kawar da wannan tsoron. Babban alkawali na ceto shine tabbacin cewa kana cikin Kristi har abada.

Sai dai kuma har yanzu muna karo da dukan ayoyin da suke koyas da cewa halayyar mai bi na gaskiya shine yana jin tsoron Allah (Ayyukan Manzanni 9:31; 10:35; Filibbiyawa 2:12; 1 Bitrus 2:17; Misalai 1:7; Mai-Wa'azi 8:12-13). To ta yaya ya kamata mu ɗauki 1 Yohanna 4:8, wadda ke koyas da cewa cikakkiyar ƙauna tana fidda tsoro? Zamu iya warware matsalar idan muka san ma'anar da Littafi Mai-Tsarki ya ba wannan kalmar ƙauna. A cikin Yohanna 14:21 mun karanta cewa:

**Wanda yake da dokokina yana kwa kiyaye su, shi ne yana ƙaunata: wanda yana ƙaunata kuma za ya zama ƙaunataccen Ubana, ni ma zan ƙaunace shi, in bayyana kaina gareshi kuma.**

An sake nanata dokar Allah a Yohanna 14:23 inda muka karanta cewa:

**Yesu ya amsa ya ce masa, idan mutum yana ƙaunata, za shi kiyaye maganata; Ubana kwa za ya ƙaunace shi, mu zo wurinsa, mu yi zaman mu tare da shi.**

Wato, an danganta ƙauna da yin biyayya da dokokin Allah, wato Littafi Mai-Tsarki. Ko da ta yaya mutum yayi ƙoƙari ya nuna ƙaunar sa ga Kristi, babban ma'aunin shine ƙaunar da sadaukarwar mutumin, biyayyar sa ga littafin shari'ar Allah wato Littafi Mai-Tsarki.

### *Cikakkiyar Kauna Na Bukatar Cikakkiyar Biyayya*

Wannan na nufin cikakkiyar ƙauna, na bukatar cikakkiyar biyayya. Sai dai kuma cikakkiyar biyyaya bata yiwuwa sai idan mun sami sabon rayayyen jiki, kuma ba za'a bamu wannan ba sai a ranar fyaucewa. Sai dai a yanzu, a cikin sabon rayayyen

ruhun mu wanda muka karɓa lokacin samun ceto, har yanzu muna rayuwa a cikin jiki wanda yake marmarin zunubi. Sabili da haka, a yanzu bamu da cikakkiyar ƙauna, sabili da haka ba zamu iya rayuwa tare da tsoro ba.

Cikin bincikenmu a baya, mun koyi wani dalili guda ɗaya da zai sa mu ji tsoro mu kuma yi rawar jiki a gaban Allah, amma zamu ƙara yin magana game da wannan. Lokacin da Dauda mutumin dake kusa da zuciyar Allah, mutumin da Allah yake ƙauna ƙwarai ya faɗi cikin zunubi, a cikin Zabura 51 Allah ya faɗa mana yadda Dauda ya ji a zuciyarsa. Dukan wannan Zabura tana bayyana yadda Dauda yaji ne sai dai zamu karanta aya ɗaya kacal. Zabura 51:11 na cewa:

**Kada ka yashe ni daga gabanka; kada kuma ka ɗauke mini ruhunka Mai-Tsarki**

Dauda ya ƙarɓi rai na har abada. Tabbatacce ne yana cikin mulkin Allah. Ta yaya zai faɗi kalmomin wannan Zabura wadda Allah Ruhu Mai-Tsarki ya bashi domin ya faɗa? Amsar na samuwa idan muka gane da irin girman hukumcin zunubi. Kowane zunubi yana bukatar hukumci. Sabili da haka idan mai bi na gaskiya ya aikata zunubi, abubuwa biyu zasu shiga tunaninsa

| |
|---|
| *Tilas ne Ubangiji Yesu Kristi ya biya dukan zunuban mu, wannan kuwa ya haɗa da zunubin da mai bi yake yi bayan ya rigaya ya sami ceto* |

Gaskiya ta fari ita ce, dole ne Ubangiji Yesu Kristi ya biya dukan zunuban mu, wannan kuwa ya haɗa da zunubin da mai bi yake yi bayan ya rigaya ya sami ceto. Gaskiya ne cewa tun da fari, Allah ya sani cewa mai bi na gaskiya zai aikata waɗannan zunuban, sabili da haka, Allah ya ɗibiya su a bisan Yesu, Yesu kuma ya fanshe su tun da daɗewa. Wannan kuma bai kawas da gaskiyar cewa wanda ya san munin zunubi da kuma irin girman alhakin da hukumcin da Allah ya ɗorawa zunubi shi ma yana aikata zunubi ba. Sabili da haka, mai bi na gaskiya yana tsoro yana rawar jiki a duk lokacin da ya aikata zunubi, dole ne a ɗora wannan zunubin ma a bisan Mai-ceto.

Gaskiya ta biyu ita ce mai bi na gaskiya yana girma cikin sanin munin zunubi da kuma babban hukumcin da shari'ar adalci ta Allah ta ɗorawa zunubi. Yana kuma da sanin cewa a duk lokacin da ya aikata zunubi, yana zaman tayaswa ne da ƙaunataccen Mai-cetonsa. Sai dai kuma, ya sani cewa Kristi ya shafe zunubansa ta wurin zubar da jininsa sabili da haka ba za'a taɓa lissafta zunubansa a bisanshi ba. Ta wani gefen kuma, ya sani cewa gafarar zunubai na samuwa ta wurin jinƙai da alherin Allah ne kawai wanda kuma bamu cancancesu ba. Sabili da haka ganin cewa ya shiga zunubi yakan sa shi ya yi rayuwa cikin tsoro da rawar jiki a gaban Allah, wannan kuma yana ƙara masa ƙarfi wajen yin ƙoƙarin ganin cewa bai yi zunubi ba, amma a maimakon haka, yana marmarin biyayyar sa ga dokokin Allah su ƙara ƙarfi.

Ta haka, mun fahimce cewa mutumin dake da ceto zai kasance da salon rayuwa na dabam, yadda kuma yake ɗaukar zunubi, Allah da kuma Littafi Mai-Tsarki zasu zama dabam da na wanda bashi da ceto.

*Ko Akwai Bege Domina?*

Shin ko abin da muka koya a baya yana nuna cewa babu sauran begen samun ceto? Eh!, hakika babu bege idan dai muna dogaro akan ƙoƙarin kanmu, bangaskiyarmu, marmarinmu ko kuma biyayyar mu domin mu taimakawa kanmu samun ceto ne. Wannan ya zama haka domin mu ɗauka cewa akwai wani abu da zamu yi da zai taimaka mana wajen samun ceto wata shaida ce ta girman kai da kuma yin watsi da dukan abin da Allah ya aikata ne. Wannan na nufin cewa muna dogaro ga shirin ceton da ba zai iya ceton kowa ba, kuma wannan yana daidai da rena kyakyawan shirin Allah na ceto.

> *Muna rayuwa ne a zamanin da Allah yake ceton ɗinbin mutanen da ba mai iya ƙirgawa*

Amma idan muka gane da shirin Allah, idan muka gane shi kaɗai ne zai iya aikata dukan abin da ake bukata domin ceto, to zamu iya samun bege, babban bege. Muna rayuwa ne a zamanin da Allah yake ceton ɗinbin mutanen da ba mai iya ƙirgawa (Ruya ta Yohanna 7:9). Har wayau, Littafi Mai-Tsarki ya

shaida cewa Allah ya zaɓi waɗansu mutane, ya kuma bada su ga Kristi, Kristi kuma ya biya dukan zunubansu, wannan ma babban dalilin bege ne ga marasa ceto.

Dukan wanda bashi da ceto kuma yake da babban marmarin samun ceto, wanda kuma ya gane cewa samun ceton sa ya dogara ne ga abin da Allah ya tsara, zai iya zama ɗaya daga cikin zaɓaɓɓu na Allah. Tun da shirin zaɓe na Allah ba a bisa cancantarmu aka kafa shi ba (domin bamu cancance shi ba), kuma kome girma ko munin zunubin mutum, zai iya kasancewa ɗaya daga cikin zaɓaɓɓu na Allah daidai da kowane wanda ya rigaya ya sami ceto. Tabbatacce ne cewa shirin zaɓe na Allah yana bada babbar ƙarfafawa ga wanda bashi da ceto wanda yake da marmarin shi ma a cece shi.

Akwai a ƙalla gaskiya guda bakwai dake a cikin Littafi Mai-Tsarki da ya kamata su zama babbar ƙarfafawa ga mutumin da yake fatan jinin Yesu zai shafe zunubansa. Mun rigaya mun yi magana akan waɗansu daga cikin waɗannan gaskiyar. Sai dai kuma sabili da muhimmancin su, zamu sake bi ta kansu kaɗan. Sun haɗa da:

1. Yau, shine ranar ceto. Mun koyi cewa yanzu Allah ba ya ceton mutane ta wurin himmar ikklisiyoyi, shugabanninsu ko kuma mutanen su. Sai dai kuma bayyananniyar koyaswar Littafi Mai-Tsarki ita ce yau Allah yana shigo da babban girbin mutane cikin mulkin Allah. Ko da yake bin diddigin wannan gaskiyar ya fi ƙarfin wannan ɗan littafin, zamu iya ambata waɗansu ayoyi kaɗan da suka tabbatar mana da haka.

A cikin Joel 2:24 mun karanta cewa:

**Masussuka za su cika da alkama** (masu bi na gaskiya) **randunan kuma za su cika sura da ruwan anab da mai har su zuba** (ceto)

A cikin Ruya ta Yohanna 7:9, Littafi Mai-Tsarki ya ce:

**Bayan wannan na duba, sai kuma ga taro mai-girma, wanda ba mai ƙirgawa, daga cikin kowane iri, da dukan kabilai da al'ummai da harsuna suna tsaye gaban kursiyin da gaban Ɗan ragon, suna yafe da fararen riguna, da ganyayen dabino cikin hannayensu**

Kana kuma Ruya ta Yohanna 7:13-14 ta faɗa mana cewa:

**Sai ɗaya daga dattiɓan ya amsa ya ce mani, waɗannan fa da suke yafe da fararen riguna, su wanene, daga ina su ke kuma? Na ce masa, Ubangiji, ka sani. Ya ce mani, su ne waɗanda suka fito daga cikin babban tsananin, suka wanke rigunansu, suka faranta su cikin jinin Ɗan ragon kuma.**

Mun karanta a cikin Habakkuk 2:14 cewa:

**Gama duniya za ta cika da sanin darajar Ubangiji, kamar yadda ruwaye sun rufe teku.**

Cikin Irmiya 33:22 mun karanta cewa:

**Kamar yadda rundunar sama ba ta ƙidayuwa, yashi a teku bashi aunuwa: hakanan zan riɓanɓanya zuriyar Dawuda bawana, da Leviyawa da ke yi mani hidima.**

Waɗannan ayoyin da ayoyi da yawa da bamu ma ambata ba suna ba kowane mutumin da bashi da ceto wanda yake zuwa gaban Allah yana neman Allah cikin ƙasƙantar da kai bege.
Domin haka, muna da tabbacin cewa a yau, ana ceton ɗinbin mutane. Kowane mutumin da bashi da ceto na iya zama ɗaya daga cikin wannan babban taron jama'ar. Babbar albarkace sanin cewa muna rayuwa a zamanin da ake ceton mutane masu yawa daga kowane ɓangare na duniya.

2. <u>Wurin da Allah yake ceto shine inda ake jin maganar Allah</u>. Littafi Mai-Tsarki A cikin Romawa 10:17 Littafi Mai-Tsarki ya furta cewa:

**Bangaskiya fa daga wurin ji ne, ji kuma daga wurin maganar Kristi.**

A yau, fiye da kowane zamani cikin tarihin ɗan adam, mutane suna da ilimi kuma suna da Littafi Mai-Tsarki a cikin yarensu. Abin ƙarfafawa ne ganin cewa kowane mutum yana iya sa kansa da kuma iyalinsa masu ceto da waɗanda ma basu da ceto ƙarƙashin sauraron maganar Allah. Zai iya yin wannan ta

wurin karatun Littafi Mai-Tsarki. A lokatai da yawa kuma, yana iya sauraron koyaswa da karatun Littafi Mai-Tsarki a radiyo irin yadda Family Radio ke yi. A gaskiya, yanayin samun ceto yayi girma a wannan zamanin fiye da kowane zamani na tarihi. Sabili da haka, mu da muke iyaye, muna so jariran mu da 'ya'yan mu su kasance wurin da zasu riƙa sauraren maganar Allah. Wannan shi ya sa radiyo ya zama wani babban kayan aiki da za'a iya yin amfani da shi domin a yaɗa Bishara ga al'ummarmu da kuma sauran ɗinbin mutanen dake ko'ina cikin duniya.

3. <u>Kristi ya zo domin ceton masu zunubi</u>. Kristi bai zo domin ceton masu adalci a ganin idanunsu ba, waɗanda suke ganin kansu tsarkaka, masu kirki, waɗanda suke ganin adalcin su zai sa Allah ya dube su da idon rahama. Kristi yazo domin ceton masu zunubi!

*Karanta labarin Ɗan fashin nan wanda aka giciye tare da Kristi abin ƙarfafawa ne*

Wani abin ƙwarin gwiwa karanta labarin ɗan fashin nan wanda aka giciye tare da Kristi abin ƙarfafawa ne. Da farko, wannan mafashin ya nuna reni ga Yesu. Mun karanta a cikin Matta 27:41-44 cewa:

**Hakanan kuma manyan malamai suna yi masa ba'a, tare da marubuta da dattiɓai, suka ce, ya ceci waɗansu ya kasa ceton kansa. Sarkin Isra'ila ne shi; shi sabko yanzu daga giciye, mu kwa mu a bada gaskiya gareshi. Yana dogara ga Allah bari ya cece shi yanzu, idan yana sonsa: gama ya ce, Ni Ɗan Allah ne. Mafasan nan kuma waɗanda aka giciye su tare da shi suka zuba masa wanann baƙar magana**

Abin sha'awa shine, yan mintoci kaɗan bayan wannan ko kuma 'yan mintoci kaɗan kafin mutuwarsa, ya roƙi Yesu yayi masa jinƙai, ya kuma karɓi amsar da ta tabbatas masa ta kuma tabbatas mana hakika a wannan lokaci ne mutumin nan ya sami ceto. Mun karanta a cikin Luka 23:39-43 cewa:

**Ɗaya a cikin mazambatan nan da aka rataye su, ya yi masa baƙar magana, ya ce, kai ba Kristi ba ne? Ka ceci kanka duk da mu. Amma ɗayan ya amsa, yana tsawata masa, ya ce, ba ka ko ji tsoron Allah ba, da shi ke shari'arka ɗaya ce da tasa? A garemu kwa hakika daidai ne, gama muna karɓan alhakin ayukanmu sosai: amma wannan mutum ba ya aika komi da ba daidai ba. Ya ce kuma, Yesu, ka tuna da ni lokacin da ka shiga mulkinka. Ya ce masa, gaskiya ina ce maka, yau kana tare da ni cikin paradise.**

Wannan babban mai zunubin yana ƙarƙashin jin maganar Allah domin ya ji Yesu yana magana da Maryamu, da Yohanna da kuma Allah da kansa. Kuma a nan take an ba wannan mugun mutumin rai na har abada. Sabili da haka kowane mutumin da bashi da ceto, kome girman zunubin sa, zai iya sanin cewa Yesu ya zo domin masu zunubi. Wannan babbar ƙarfafawa ce!

4. Yesu ba ya tara. Wannan na nufin cewa babu wani jinsi na mutane da yafi wani zarafin samun ceto. Jama'a zasu iya yin watsi da mutum, mutane na iya ƙyamar sa, amma a cikin Littafi Mai-Tsarki, Allah ya faɗa mana labarin mutanen da suka zama abin ƙyama ga jama'a waɗanda suka sami ceto a zamanin Yesu. Misalin wannan shine ceton Basamariyan nan (Yohanna 4:4-42), Zakka mai karɓar haraji (Luka 19:2-8), Kuturun nan (Luka 17:12-19), Mai laifin da aka kashe sabili da laifin sa (Luka 23:39-43) da kuma macen nan da aka kama cikin zina (Yohanna 8:1-11). Jama'a suna ganin dukan waɗannan a matsayin ƙazamai, amma Allah ya ceci kowane ɗayansu. A nan muna gani a fili cewa Allah ba mai tara bane. Wannan labari ne mai daɗi ga dukan wanda bashi da ceto.

5. <u>Allah Mai-jinƙai ne.</u> gaskiya ne cewa yanzu ba a samun jinƙai a cikin ikklisiyoyi inda fastocinsu, dattijan su da malaman Littafi Mai-Tsarkin suke yiwa waɗannan mutanen hidima. Wannan mugun abu ne. Amma a waje da majami'un, Allah yana nuna jinƙansa wanda bashi da misali a ko'ina cikin duniya. Allah, Allah Mai-jinƙai ne.

Mun karanta a Zabura 103:8 cewa:

**Ubangiji cike da tausayi yake, mai-nasiha, Mai-jinkirin fushi, mai-yalwar jinƙai kuma**

Haka kuma, a cikin Makoki 3:31-32 mun karanta cewa:

**Gama Ubangiji ba ya yasda mutum har abada ba. Gama ko da ya sa baƙin ciki, duk da haka za shi yi juyayi bisa ga yawan jinƙansa**

A cikin Joel 2:13, Allah kuma ya zaiyana cikin jinƙansa cewa:

**Ku tsaga zukatanku ba tufafinku ba, ku juyo wurina Ubangiji Allahnku: gama shi mai alheri ne, cike da juyayi, mai jinkirin fushi, mai-yalwar jinƙai, yana sake nufinsa a kan masifan da ya shirya.**

6. Kowanne ɗayanmu zai iya nunawa Allah zafin marmarin samun ceton da yake da shi. Za mu iya yin roƙo, nema, mu kuma yi roƙo ga Allah domin ceto. Addu'a ga Allah aiki ne da muke yi, sabili da haka mun sani cewa yin addu'a ga Allah ba zai tabbatar mana ko kuma taimaka mana samun ceto ba. Sai dai zamu iya sanin cewa yayinda muke kuka ga Allah, zai iya sanin marmarin da muke da shi na samun ceto.

Yesu ya bada misali na mai karɓar harajin nan wanda yayi addu'a ga Allah domin jinƙai wanda muke karantawa a Luka 18:13-14:

**Amma shi mai-karɓan haraji, da ya ke tsaye daga nesa, ba ya yarda ya tada ko idanunsa sama, amma sai ya bugi ƙirjinsa, ya ce, ya Allah, ka yi mani jinƙai, ni mai zunubi ne. Ina ce maku, wannan mutum ya tafi gidansa baratacce ne bisa ga wancan: gama dukan wanda ya ɗaukaka kansa za shi ƙasƙanta; amma wanda ya ƙasƙantadda kansa za shi ɗaukaka.**

7. Bai kamata mu fidda begen samun ceto ba. Idan Allah yayi niyyar ceton, zai yi wannan a lokacinsa. Zai iya ceton mu da sauri a cikin rayuwarmu ko kuma zai iya bari sai muna kusa da

mutuwa. Idan dai har Allah yana da niyyar ceton mu, to kada muyi kuskuren faɗawa Allah lokacin da zai cece mu.

*Idan Allah yayi niyyar ceton mu, zai yi wannan a lokacinsa*

Mun karanta a Makoki 3:26 cewa:

**Abu mai kyau ne mutum shi yi bege, shi saurari ceton Ubangiji a natse**

Haka kuma a Zabura 62:5-8 Allah ya ƙarfafa mu da cewa:

**Raina, ka yi sauraro ga Allah kaɗai, gama daga gareshi begena ya ke. Shi kaɗai ne Dutse kuma mai cetona, hasumiyata kuma; ba zan jijjigu ba. A wurin Allah cetona ya ke da girmana kuma; pa na ƙarfina, da mafakata, cikin Allah ne. Ku al'ummai, ku dogara gareshi ko wanne loto, ku zazzage zuciyarku a gabansa: Allah mafaka ne a garemu.**

Yayinda mutum yake sauraron Ubangiji cikin natsuwa, ba wuya ya cika da ganin nawa. Samun ceto wani abu ne mai muhimmanci ƙwarai. Kasancewa babu ceto mugun abu ne.

Allah ya bamu ƙarfafawa tare da alkawali a cikin Filibbiyawa 4:6

**Kada ku yi alhini cikin kowane abu, ta wurin addu'a da roƙo tare da godiya, ku bar roƙe-roƙenku su sanu ga Allah.**

Kana sai Allah ya bamu tabbaci a cikin Filibbiyawa 4:7:

**Salama kwa ta Allah wadda ta fi gaban ganewa duka, za ta tsare zukatanku da tunaninku cikin Kristi Yesu.**

A nan Allah yana ƙarfafa mu ta wurin ƙarfafa mu, mu dogara gareshi shi kaɗai. yana ƙarfafa mu mu ɗora dukan damuwar mu a bisansa. Shi kuma mai adalci ne abin dogaro kuma da zai aikata kyakyawan nufinsa. Kamata yayi mu jingina ga karfafan hannuwansa.

A yanzu, zamu iya ji daga Allah yayinda muke ci gaba da karatun Littafi Mai-Tsarki a hankali muna kuma yin addu'a. A duk lokacin da damuwa ta kama mu, zamu iya zuwa gaban dakalin alherin Allah akai-akai muna faɗa masa dukan damuwar mu. Allah mai jinƙai ne.

A cikin Zephaniah 2:3, Allah ya ba marasa ceto wata babbar ƙarfafawa. A wurin mun karanta cewa:

**Ku biɗi Ubangiji ku dukan masu tawali'u** (masu ƙasƙantar da kansu) **na duniya, ku waɗanda kuka kiyaye shari'arsa: ku biɗi adilci, ku biɗi tawali'u: ko watakila a ɓoye ku a cikin ranar fushin Ubangiji.**

Sabili da haka, kila, Allah ya cece ku.

Farawa 9:6, 19
Farawa 15:6, 39, 41, 4
Farawa 22, 21

Fitowa 31:13-14, 22

Lissafi 15:40, 46, 49
Lissafi 15:32-36, 22
Lissafi 22:12-13, 18, 25
Lissafi 22 da 23, 19

Kubawar Shari'a 4:29, 29
Kubawar Sharia 28:1,
28:15, 30:6-16, 25
Kubawar Shari'a 30:6, 38

1 Samu'ila 10:9-12, 18, 25

1 Labarbaru 10:13, 25

Zabura 34:9, 55
Zabura 51:54, 58
Zabura 51:11, 58
Zabura 62:5-8, 65
Zabura 103:8, 63
Zabura 112:1, 55
Zabura 119, 53
Zabura 119:10, 53
Zabura 119:16, 53
Zabura 119:24, 53
Zabura 119:47, 53
Zabura 119:77, 53
Zabura 119:97, 53
Zabura 138:2, 3
Zabura 139:23-24, 24

Misalai 1:7, 57
Misalai 3:7, 55
Mai Wa'azi 8:12-13, 57
Mai Wa'azi 8:13, 56

Ishaya 53:6, 6
Ishaya 57:11-12, 56
Ishaya 63:5, 6
Ishaya 66:24, 19

Irmiya 5:24-25, 56
Irmiya 17:9, 30, 34
Irmiya 23:39-40, 24:10, 19
Irmiya 29:17-19, 27
Irmiya 29:18-19, 28
Irmiya 31:8-9, 27
Irmiya 33:22, 61
Irmiya 36:1-4, 3
Irmiya 44:9-10 ,56

Makoki3:26, 65
Makoki 3:31-32, 63

Ezekiel 22:30, 6
Ezekiel 33:11, 19
Ezekiel 36:24-27, 34
Ezekiel 37, 11,35
Ezekiel 37:1-14, 17

Joel 2:12-14, 26
Joel 2:13, 64
Joel 2:13-14, 44
Joel 2:24, 60

Jonah 3, 44
Jonah 3:5, 38
Jonah 3:8-10, 44
Jonah 3:9, 26,29
Jonah 3:10, 15

Habakkuk 2:14, 61

Zephaniah 2:3, 44,66

Matta 4:14,8:17,12:17, 43

Matta 5:22, 19
Matta 7:22, 15
Matta 9:16, 11
Matta 15:19, 9,34
Matta 23, 28
Matta 27:41-44, 62
Matta 27:46, 7
Matta 4:33-34, 48
Matta 7:21, 30
Matta 13:13, 32

Luka 13:24, 20
Luka 17:12-19, 63
Luka 18:13, 26
Luka 18:13-14, 64
Luka 19:2-8, 63
Luka 19:41, 18
Luka 23:9-43, 5
Luka 23:39-43, 62, 63

Yohanna 3:3 da 7, 11
Yohanna 3:5, 13
Yohanna 3:16, 35
Yohanna 4:4-42, 63
Yohanna 4:10-15, 14
Yohanna 6:37, 5
Yohanna 6:44, 18,19
Yohanna 7:38, 14
Yohanna 8, 5
Yohanna 8:1-11, 63
Yohanna 8:9, 18,24
Yohanna 8:44, 47
Yohanna 11: 12
Yohanna 11:39, 10,17,35
Yohanna 14:21, 57
Yohanna 14:23, 11,57

Ayyukan Manzanni 8:13-23, 34
Ayyukan Manzanni 9:31, 10:35, 57
Ayyukan Manzanni 16"31, 35

Romawa 2:11, 5
Romawa 2:13-15, 1
Romawa2:14-15, 18,24
Romawa 2:15, 19
Romawa 3, 35
Romawa 3:10-12,4, 17
Romawa 4:3, 39,42
Romawa 4:9, 39
Romawa 4:11, 37,38
Romawa 7:21-24, 51
Romawa 8:9, 52
Romawa 8:35-39, 51
Romawa 9:15, 5
Romawa 9:31-32, 25
Romawa 10:9-10, 33
Romawa 10"13, 29,31
Romawa 10:17, 14,28,61

1Korantiyawa 2:13, 29
1Korantiyawa15, 32
1Korantiyawa 15:52, 11

11Korantiyawa 2:4, 44
11Korantiyawa 5:8, 13
11Korantiyawa 5:17, 11
11Korantiyawa 11:7, 44
11Korantiyawa 11:13, 15,46
11Korantiyawa 11:14, 47
11Korantiyawa 11:15, 47
11Korantiyawa 13:5, 23

Galatiyawa 2, 36
Galatiyawa 2:16, 15,37,42,44
Galatiyawa 3, 36
Galatiyawa 3:2, 36,37
Galatiyawa 3:6, 39,42
Galatiyawa 3:11, 37
Galatiyawa 3:16, 51

Afisawa 1:3-55, 4
Afisawa 1:4, 5
Afisawa 1:13, 7-38

| | |
|---|---|
| Afisawa 2:1-3, | 13 |
| Afisawa 2:3 | ,9 |
| Afisawa 2:8, | 37 |
| Afisawa 2:8-9, | 15 |
| Afisawa 6:9, | 5 |
| | |
| Filibiyawa 2:12, | 54,57 |
| Filibiyawa 3:20, | 52 |
| Filibiyawa 4:6, | 65 |
| Filibiyawa 4:7, | 65 |
| | |
| Kolosiyawa 1:12-13, | 52 |
| Kolosiyawa 3:25, | 5 |
| | |
| ITassalonikawa 1:3,16, | 40 |
| ITassalonikawa 4, | 13 |
| | |
| I1Tasalonikawa 1:11, | 16,40 |
| | |
| Ibraniyawa 4:11, | 20 |
| | |
| Yakub 2:23, | 42 |
| | |
| 1Bitrus 1:5, | 32 |
| 1Bitrus 1:5, | 32 |
| 1Bitrus 1:23, | 11 |
| 1Bitrus 2:17, | 57 |
| 11Bitrus 1:21: | 3 |
| 11Bitrus 2:15-16, | 25 |
| 11Bitrus 3:18, | 52,54 |
| | |
| 1Yohanna 2:3-5, | 54 |
| 1Yohanna2:3-6, | 24 |
| 1Yohanna 3:9, | 50 |
| 1Yohanna 4:18, | 56,57 |
| | |
| Ruya Ta Yohanna 7:9, | 59,60 |
| Ruya Ta Yohanna 7:13-`4, | 60 |
| Ruya Ta Yohanna 13:8, | 8,9,17 |
| Ruya Ta Yohanna 19:11, | 37,45 |
| Ruya Ta Yohanna 20:14-15, | 10 |

## Ka ziyarci yanar gizon mu a
## **www.familyradio.com**

Shirye shiryen Family Radio na Littafi Mai-Tsarki suna nan a internet awa 24 kowace rana, dukan ranakun mako. Zaka sami tarin shirye shiryen mu a wurin waɗanda suka ƙunshi shirin yaɗa shirye shirye a tashar radiyo mai gajeren zango, binciken Littafi Mai-Tsarki, da kuma Littafi Mai-Tsarki a rubuce ko a karance cikin harsuna da yawa.

Zaka iya sauraren shirye-shiryen Family Radio ko kuma kana iya shirye shiyen. Akwai kuma karatun da binciken ayoyin Littafi Mai-Tsarki daga yanar gizon mu.

Idan kana son ka karɓi jerin shirye shiryen mu, sanarwa game da koyon Littafi Mai-Tsarki ta wasiƙa, littattafai kyauta, to sai ka rubuto zuwa ga

Family Radio
Oakland, CA 94621, USA

Addrreshin computan mu shine international@familyradio.com
Adireshin computan mu shine international@familyradio.com